# IYALI AMANA NE DAGA ALLAH



**Bayanai A Kan Mas'alolin Da Suka Shafi Aure, Zamantakewar Iyali, Reno Da Tarbiyyar 'Ya'ya A Cikin Musulunci**


**Na**

**WAZIRIN KATSINA Na 5**

**Prof. Sani Abubakar Lugga, MFR**

Lokacin da Allah (SWT) Ya nufe mu da kafa Jami'ar Musulunci ta farko a Najeriya a Katsina a shekarar 2005 Miladiyya, sai na riƙa koyar da Darasin "General Studies" wanda ya shafi rayuwar Musulmi ta yau-da-kullum ga ɗalibai kimanin 1,200, daga samari har zuwa magidanta. Kuma tun daga 2002 na ke sauraren irin koke-koken da jama'a ke gabatarwa a Majalisar Mai Martaba Sakin Katsina. A waɗannan wurare biyu ne na lura da tsananin rashin ilmin mutane a kan rayuwar yau-da-kullum. Domin haka, na wallafa Littafi mai suna "Yi Ma Kan Ka Hisabi" a 2016 mai ɗauke da bayanai a kan muhimman abubuwan rayuwa da na fahimci sun fi neman ilmantarwa. Domin wancan Littafin yana da girma kwarai, sai na tsakuro abin da ya shafi aure da zamtakewar iyali daga cikin sa, na yi wasu ƙare-ƙare da gyare-gyare na wallafa wannan ƙaramin Littafin. Allah Ya sa mu dace, domin Shi kaɗai ne Masani, ameen.

# IYALI AMANA NE DAGA ALLAH



**Ya ku wadanda kuka yi imani! Ku kare kawunan ku da na iyalan ku daga wata Wuta (Jahannama) wadda makamashin ta mutane da duwatsu; wadda aka sanya Mala'iku masu tsanani su kula da Ita; kuma basu wasa da Umurnin da Allah Ya basu, suna aikata duk abinda aka yi masu umurni da shi nan ta-ke! (Qur'an 66:6)**

WAJIBI NE MUSULMI SU KULA DA AYALANSU A MUSULUNCE!

# IYALI AMANA NE DAGA ALLAH





# IYALI AMANA NE DAGA ALLAH





# IYALI AMANA NE DAGA ALLAH

**Na:**
**Professor Sani Abubakar Lugga, MFR**
**Wazirin Katsina Na 5**
**Professor of Management Studies**
**Doctor of Philosophy in Conflict Management**
**Fellow of the Nigerian Institute of Management**
**Fellow of the Institute of Management Consultants (Nigeria)**
**Fellow of the Institute of Professional Financial Managers (UK)**
**Fellow of the London Graduate School, London, United Kingdom**
**Key Founder and former Senior Lecturer, Al-Qalam University, Katsina**
**Visiting Prof., Ecole Superieure Universitaire, Cotonou, Benin Republic**
**Visiting Professor at St. Clements Private Swiss University, Switzerland**
**Committee Member, Nigeria Supreme Council for Islamic Affairs**
**Committee Chairman, Jama'atuNasril Islam, Kaduna, Nigeria**
**Member of Sultan Foundation for Peace and Development**
**Executive Member, Interfaith Initiative for Peace, Nigeria**
**Ambassador of Universal Peace Federation, New York**
**Member of Professors World Peace Academy, Korea**

**www.books.luggaweb.com**

**AN WALLAFA WANNAN LITTAFI DOMIN ILMANTARWA BA DON SAYARWA BA!**

**Haƙƙin Mallaka** © Prof. Sani Abubakar Lugga
© **Copyright:** Prof. Sani Abubakar Lugga

**ISBN 978-978-778-070-1**

**Ɗab'in Maɗaba'ar Lugga**
Gidan Lugga, Titin Kofar Marusa, Katsina,
Jihar Katsina, Najeriya.

**Ramadan 1446 Hijrah**
**March (Maris) 2025 Miladiyya**

# ABUBUWAN DA KE CIKI


| BABI | | SHAFI |
|---|---|---|
| | GABATARWA | 8 |
| ƊAYA | MUHIMMANCIN AURE A MUSULUNCI | 10 |
| | Umurnin Allah Da Annabi (SAW) A Kan Aure | 10 |
| | Shin, Yin Aure Wajibi Ne? | 12 |
| BIYU | MAS'ALOLIN AUREN DOLE | 14 |
| | Hadisin Annabi (SAW) A Kan Auren Dole | 14 |
| | Fatawowin Manayan Malamai Kan Auren Dole | 15 |
| UKKU | WALICCI WAJEN YIN AURE | 20 |
| HUƊU | NEMA DA ƊAURA AURE | 25 |
| BIYAR | HAKƘOKIN MA'AURATA | 30 |
| | Haƙƙoƙin Da Ma'aurata Suka Yi Tarayya | 31 |
| | Haƙƙoƙin Mata A Kan Mijin Ta | 31 |
| | Haƙƙoƙin Miji A Kan Matar Sa | 32 |
| SHIDDA | WASU MUHIMMAN MAS'ALOLI | 33 |
| | Sai Mai Hali Yin Aure Ne Zai Yi Aure? | 33 |
| | Wane Irin Gida Ne Za'a Sanya Matar Aure? | 35 |
| | Ana Iya Haɗa Matan Aure A Gida Guda? | 37 |
| | Mene Ne Hukuncin Ciyarwa Da Tufatarwa? | 41 |
| | Tilas Ne Matar Aure Ta Dafa Abinci? | 42 |
| | Menene Hukuncin Miji Ya Yi Ma Matar Aure Abubuwa Kamar Yadda Ta Saba A Gidan Su? | 45 |
| BAKWAI | TARBIYYAR 'YA'YA | 46 |
| TAKWAS | MAS'ALOLIN SAKIN AURE | 51 |
| TARA | RENON YARA DA KULA DA DUKIYAR SU | 58 |
| | RUFEWA | 66 |


**A Lura Cewa An Fara Buga Wannan Littfai Da Sunan "HATTARA MA'AURATA" A Shekarar 1438 AH (2017 AD).Yanzu An Inganta Shi Da Sabon Suna**

# GABATARWA

## بسم الله الرحمن الرحيم

## نحمده تعالي ونشكره علي نعمه والصلاة والسلام علي رسوله الكريم وعلي آله وصحبه أجمعين

*Assalamu Alaikum wa Rahmatul Lahi Ta'ala wa Barkatuhu,*

Domin Musulmi Ma'aurata su samu natsuwa su daidaita sahun auren su da renon 'ya'yan su ta turbar da Musulunci ya tsara ne aka wallafa wannan Littafin. An duba mas'alolin da suka fi shafuwar Musulmi Ma'aurata a cikin wannan zamani kuma aka kawo bayanai a kan su kamar yadda suke bayyane a cikin *Kitab-was-Sunnah.* An yi ƙoƙari an sauƙaƙa bayanan domin ko wane Musulmi ya samu damar fahimtar su domin ya yi aiki da su gwargwadon iyawar sa. Kuma a lura cewa na ciro wannan Littafi ne sannan na yi masa wasu ƙare-ƙare da gyare-gyare daga wani babban Littafi da na wallafa a shekarar 2016 Miladiyya mai suna, "YI MA KAN KA HISABI Kamin Allah Ya Yi Maka"; wanda ya ƙunshi mas'alolin rayuwa daban-daban da suka addabi Musulmi a wannan zamanin.

**FAƊAKARWA DA ROKO:** Allah Ya sa duk abinda aka rubuta a wannan Littafi ya zama alheri gare mu baki ɗaya, kuma Allah Ya gafarta mana duk wani kuskure da aka yi a cikin Littafin, domin duk ɗan Adam ajizi ne. Kuma ina roƙon duk wanda ya karanta wannan Littafi da ya yi aiki da abinda ke cikin sa wanda ya yi muwafaƙa da *Kitab-was-Sunnah*, kuma ya gyara duk abinda bai yi muwafaƙa da su ba; bayan haka ya aiko ma ni ko ya aika ma Kamfanin Ɗab'in Littafin domin a gyara. **Allah Shi ne Masani.**

**GODIYA DA FATAN ALHERI:** Ina roƙon Allah Ya saka ma duk waɗanda suka taimaka wajen samuwar wannan Littafi da alheri; musamman waɗanda suka dubaBabban Littafin "YI MA KAN KA HISABI" kuma suka yi gyare-gyare da bada shawarwarin inganta shi. Waɗannan bayin Allah sun haɗa da Sheikh Imam Abba Muhammad Aliyu (Babban Limamin Masallacin Juma'a a Katsina), Sheikh Imam Abubakar Ibrahim Charanchi (Shugaban Kolejin Musulunci ta Usman Fodio kuma Babban Limamin Juma'a a Katsina), Sheikh Labaran Imam Saulawa (Babban Malami a Kolejin Musulunci ta Usman Nagogo, Katsina), Prof. Muhammad Sagir Adam (Shugaban Sashen Larabci a Jami'ar Musulunci ta Katsina), Hon.Justice Nuruddeen Abbas Mashi (Joji a Kotun Ɗaukaka Kara ta Shari'ar Musulunci ta Jihar Katsina), Dr. Abubakar Sani Lugga (Likita a Asibitin Koyarwa ta Gwamnatin Tarayya a Katsina kuma Hafizin Al-Kur'ani) da sauran bayin Allah da fili ba zai isa a zayyana dukkan sunayen su ba a nan.

Ina godiya ga mata na, Binta da Hadiya da Azhar; da 'ya'ya na, da jikoki na, da sauran iyalan gida na da suke yi mani biyayya da kyautatawa kamar yadda Allah Ya ce a yi. Ina yi masu addu'ar Allah ya Yi masu albarka kuma Ya saukar masu da alherin Shi, Duniya da Lahira,*Ameen.*

Ina roƙon Allah Ya jiƙan iyayen mu, Alhaji Abubakar Lugga da Hajiya A'isha, waɗanda suka rene mu kuma suka yi mana tarbiyya irin ta addinin Musulunci. Ina roƙon Allah Ya jiƙan matata Ummah da ɗiyata Fatima. Ina roƙon Allah Ya sada mu da su da dukkan Musulmi a Aljannar Firdausi, *ameen.*

*Wassalamu Alaikum wa Rahmatul Lahi Ta'ala wa Barkatuhu.*

# Babi Na Ɗaya
# MUHIMMANCIN AURE A MUSULUNCI

Aure muhimmin al-amari ne a cikin addinin Musulunci kuma yana da sharuɗɗa da yawa waɗanda tilas ne a bi su tun daga lokacin da mace da namiji suka fara ganin juna har zuwa lokacin da aka ɗaura aure kuma mata ta tare gidan mijinta har ya zuwa ƙarshen rayuwarsu a Duniya. Idan ma rabuwa ma'aurata suka yi ta hanyar sakin auren, to, nan ma akwai sharuɗɗa na sakin auren da abubuwan da za su biyo bayan wannan.

## UMURNIN ALLAH (SWT) A KAN AURE

Allah (SWT) Ya faɗa a cikin al-Kur'ani Mai Girma, aya ta 1, a suratul Nisa'i cewa,

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُواْ رَبَّكُمُ ٱلَّذِي خَلَقَكُم مِّن نَّفۡسٖ وَٰحِدَةٖ وَخَلَقَ مِنۡهَا زَوۡجَهَا وَبَثَّ مِنۡهُمَا
رِجَالٗا كَثِيرٗا وَنِسَآءٗۚ

*Ya ku mutane, ku ji tsoron Ubangijinku, wanda Ya halicce ku daga rai guda (Annabi Adam) kuma Ya halicci* ***matarsa*** *(Hawwa'u) daga gare shi, sannan Ya sanya'ya'ya masu yawa daga gare su, maza da mata.*

Kuma a aya ta 3 a wannan sura, Allah (SWT) Ya ce,

فَٱنكِحُواْ مَا طَابَ لَكُم مِّنَ ٱلنِّسَآءِ مَثۡنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَۖ فَإِنۡ خِفۡتُمۡ أَلَّا تَعۡدِلُواْ فَوَٰحِدَةً
أَوۡ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُمۡۚ ذَٰلِكَ أَدۡنَىٰٓ أَلَّا تَعُولُواْ

*Ku auri abinda ya yi maku daɗi daga mata, biyu, ko ukku, ko huɗu. Ama idan ku ka ji tsoron (cewa) ba za ku yi adalci ba (a tsakanin su), to, ku auri ɗaya ko kuma abin da hannayen ku suka mallaka (watau kuyangi). Haka shi ne ya fi kusa da rashin zalunci.*

## UMURNIN MANZON ALLAH (SAW) A KAN AURE

Hadisi na 1, a cikin kashi na 7 (Vol. 7) na Sahih Al-Bukhari ya bayyana cewa Anas bin Malik ya ruwaito cewa wasu mutane ukku sun je gidan Manzon Allah, Annabi Muhammadu (SAW) suka tambayi yadda ya ke yin ibada. Da aka yi masu bayani sai suka rena tasu ibadar suka ce, "ina mu ke, idan Annabi (SAW) da Allah Ya yafe masa zunubbansa da ya yi da waɗanda zai yi, yana ibada haka?" Sai ɗayansu ya ce shi daga yau zai ta yin Sallah dukkan dare baya barci. Ɗaya kuma ya ce shi zai ta Azumi kullum duk tsawon shekara. Ɗaya kuma ya ce shi ba zai yi aure ba har abada. Lokacin da Manzon Allah (SAW) ya fito sai ya tambayi mutanen nan ukku cewa, *"shin ku ne ku ka faɗi kaza da kaza?"* Suka amsa cewa lallai su ne. Sai Annabi (SAW) ya faɗa masu cewa, " *Wallahi na fi ku bautar Allah kuma na fi ku tsoron Allah, amma ina yin azumi kuma ina aje azumi, kuma ina yin barci, kuma ina auren mata. Wanda duk ya ƙyamaci Sunnah ta, to, baya tare da ni".* Abin kula a cikin wannan hadisi shi ne inda Annabi (SAW) ya ce,

**...وَأَتَزَوَّجُ النِّسَاءَ ، فَمَنْ رَغِبَ عَنْ سُنَّتِى فَلَيْسَ مِنِّى**

*Kuma ina **auren mata**. Wanda duk ya ƙyamaci Sunnah ta, to, baya tare da ni.*

A wani muhimmin Hadisin Manzon Allah (SAW), Buhari da Muslim sun ruwaito cewa, Annabi (SAW) ya ce,

**يَا مَعْشَرَ الشَّبَابِ مَنِ اسْتَطَاعَ مِنْكُمُ الْبَاءَةَ فَلْيَتَزَوَّجْ فَإِنَّهُ أَغَضُّ لِلْبَصَرِ وَأَحْصَنُ لِلْفَرْجِ وَمَنْ لَمْ يَسْتَطِعْ فَعَلَيْهِ بِالصَّوْمِ فَإِنَّهُ لَهُ وِجَاءٌ**

*Ya ku wannan rukunin matasa! Wanda duk ke da hali a cikin ku, to, ya yi aure domin shi ne zai sanya ya kame daga kallo (na matan da su dace ya kalla ba) da kiyaye farji, wanda duk bai samu hali ba, to, na umurce shi da yin azumi zai zama mai karya a gareshi.*

Ahmad da Ibn Hibban sun ruwaito Manzon Allah (SAW) yana cewa,

تَزَوَّجُوا الْوَدُودَ الْوَلُودَ فَإِنِّى مُكَاثِرٌ بِكُمُ الأُمَمَ يوم القيامة

*Ku auri masoyan ku, kuma ku hayayyafa da yawa, domin in yi alfahari da cewa al-umma ta, ita ta fi ta kowa yawa a Lahira.*

Faɗar Allah (SWT) da faɗar Manzon Allah (SAW) sun tabbatar da muhimmancin yin aure a cikin Musulunci. Ba shakka, aure Sunnah ne, amma da an yi niyyar yin shi, har zuwa tarewar matar gidan mijinta, har zuwa tsawon rayuwarsu a duniya, sai Wajibai su shigo waɗanda karya su zai jaza manyan zunubbai da hukunce-hukunce.

## SHIN YIN AURE WAJIBI NE?

Babu shakka, yin aure Sunnah ce ta Manzon Allah (SAW). Amma wani gagarumin al-amari shi ne, a yi la'akkari da cewa, a cikin Musulunci mutane basu yaɗuwa, watau ba'a haihuwa, sai da aure. Ashe idan babu aure to sai wata rana a tashi babu Musulmi ko ɗaya domin Musulunci bai yarda da samun 'ya'ya ta hanyar da ba aure ba, watau ta hanyar zina.

Kuma a lura da cewa Allah (SWT) cewa Ya yi Ya halitta ma Annabi Adam (AS) "**matar aure**" (watau **وخلق منها زوجها**) ba cewa Ya yi ba **mace** (watau **المرأة**). Sannan a lura da cewa, Annabi (SAW) ya ce yana yin **aure** kuma aure Sunnah ne, kuma wanda duk ya ƙyamaci Sunnar sa to baya tare da shi. Kuma Annabi (SAW) ya umurci matasa su yi aure muddin suna da halin yi. Sannan Annabi (SAW) ya ce yana so Musulmi su yi aure kuma su hayayyafa domin ya yi alfahari da cewa al-ummar sa ta fi ta kowa yawa a lahira.

**Idan aka duba waɗannan dalillai, ana iya cewa aure Sunnah ce wajiba ga duk Musulmin da ya cika ƙa'idojin yin sa. Domin idan babu aure ashe wata rana babu sauran Musulmi 'yan halas sai dai 'yan zina, kada Allah Ya kawo wannan lokaci, ameen.**

Sheikh Ahmad Bello Dogarawa ya yi bayanai masu kyau a kan muhimmancin yin aure a cikin littafin shi mai suna, "Tarbiyyar 'Ya 'Ya a Musulunci". Shehun Malamin ya ce Aure aya ce daga cikin ayoyin Allah, kuma ni'ima ce daga cikin ni'imomin Shi. An shar'anta aure a Musulunci, aka ƙarfafa shi, aka kwaɗaitar da yin shi, aka hana yin *tabattul* (aƙidar rashin yin aure saboda a samu damar yin bautar Allah kaɗai). Musulunci ya bayyana cewa barin yin aure domin a samu damar yin ibada ya saɓa wa Sunnar Manzon Allah (SAW).

**Aure na da manufofi da fa'idodin da suka haɗa da:**

1. Biyayya ga Allah (SWT) da rayar da Sunnar Annabi (SAW)
2. Samun ladar ciyar da iyali.
3. Kamewa daga yin zina, da tsare mutunci.
4. Samar da iyali da taimakawa wajen yawaita al'umma tsarkakkiya.
5. Ɗorewar jinsin 'yan Adam na halas ba na haram (zina) ba.
6. Samun 'ya'ya na ƙwarai da za su riƙa yi wa iyayen su addu'a bayan mutuwar iyayen.
7. Samun natsuwa da sukuni da kwanciyar hankali.
8. Biyan buƙatar sha'awa ta ɗabi'a (watau yin jima'i)
9. Samun ladar yin tarbiyya da ɗaukar ɗawainiyar 'ya'ya.
10. Kai wa ga matsayin kamala a cikin mutane.

# Babi Na Biyu
# MAS’ALOLIN AUREN DOLE

Duk da muhimmamcin aure a Musulunci, al-adu da ɗabi’un ƙasashe da ƙabilu suna neman rusa sharuddan da Musulunci ya shinfiɗa. Misali, ana ta fama da tilasta ma mata su auri mazajen da basu so, kuma suma mazajen haka. Kotunan Shari’ah da Majalisun Sarakuna kullum cike suke da ƙararraki a kan **Auren Dole**.Mas’alar tilastawa ‘yan mata (watau budurwoyi) su auri mazajen da basu so, ta zama babban al-amari a zamanin yau. Su ma samari (‘yan-maza) a kan samu wannan mas’ala. Sai dai a wannan Babi za’a maida hankali wajen maganar auren tilas akan budurwa ba akan saurayi ba, domin wannan al-amari akan 'yan-mata ya fi yawa kuma ya fi aibi.

## HADISIN ANNABI (SAW) A KAN AUREN DOLE

Hadisi na 67, a cikin kashi na 7 (Vol. 7) na Sahih Al-Bukhari ya bayyana cewa Abu Huraira (RA) ya ce Manzon Allah, Annabi Muhammadu (SAW) ya faɗi cewa,

**لاَ تُنْكَحُ الْبِكْرُ حَتَّى تُسْتَأْذَنَ ، وَلاَ الثَّيِّبُ حَتَّى تُسْتَأْمَرَ.فَقِيلَ يَا رَسُولَ اللَّهِ كَيْفَ إِذْنُهَا قَالَ إِذَا سَكَتَتْ. رواه الَبخاري**

*Ba za'a aurar da bazawara ba sai da izinin ta kuma ba za'a aurar da budurwa ba sai ta amince"* sai Sahabbai suka ce, "ya Manzon Allah, yaya zamu san cewa budurwar ta amince? Sai Annabi (SAW) ya ce, *"idan aka tambaye ta, sai ta yi shiru, to, ta amince".*

Aisha (RA) ta tambayi Annabi (SAW) cewa, "Ya Manzon Allah, budurwa na da kunya (bata iya bada amsar tambaya)". Sai Annabi (SAW) ya ce, *"ai idan ta yi shiru, to, ta amince*". Sahih Al-Bukhari kashi na 7, hadisi na 68 ya yi bayani a kan wannan.

Hadisi na 70, a cikin kashi na 7 (Vol. 7) na Sahih Al-Bukhari ya bayyana cewa Abdul Rahman bin Yazid (RA) da Majammi bin Yazid (RA) sun ruwaito cewa wani mutum mai suna Khidam ya aurar da ɗiyarsa ba da son ranta ba, sai Annabi (SAW) ya warware auren.

## FATAWOYI A KAN AUREN DOLE

### Bayanin Sheik Ibn Asim

Sheik Abubakar ibn Asim al-Garnadi al-Andulusi ya yi dogon bayani a kan tilasta ma budurwa ta yi aure a cikin littafinsa *"Tuhufatul Hukkam".* A shafi na 160, na fassarar wannan littafi da Alƙalin Alƙalai Usman Muhammad Daura ya yi, an yi bayani kamar haka:-

*"Budurwa kuma wadda ba'a yi mata tilas, ita ma ba za'a ɗaura mata aure ba sai da yardar ta, ko ta yi magana ta ce ta yarda, ko kuma idan aka tambaye ta, ta yi shiru, to sai a ɗauka ta yarda, amma kuma ana so a nuna mata cewa, idan fa ta yi shiru, ma'anarsa ta yarda ke nan, kamar yadda Ma'aiki (SAW) ya ce".*

### Fatawar Sheik Bin Baz

Marigayi Sheik bin Baz shi ne Shugaban Kwamitin Malaman Islama na Duniya a ƙarkashin Hukumar Musulmi ta Duniya (World Islamic League) masu yin taro duk shekara a ƙasar Saudiyya domin yin fatawoyi. Kuma shi ne Babban Muhuti (Grand Mufti) na ƙasar Saudiyya wanda ke da ikon soke duk abinda Gwamnatin Saudiyya ta yi muddin ya saɓa ma Islama. Sheik bin Baz ya yi bayani a kan mas'alar tilasta ma budurwa ta auri wanda bata so har kusan shafi ukku (shafi na 167 zuwa na 169) a cikin littafin da aka fassara da harshen Turanci mai suna **"Fatawa Regarding Women"** (watau *Fatawa a kan Mata*). A cikin

bayanan da Malamin ya yi, an fassara abinda ya ce a cikin littafin da aka ambata a sama, da harshen Turanci kamar haka,

"*Neither the father, nor anyone may force a woman who is under his guardianship to marry a man that she does not want to marry. In fact, her permission must be sought. The Messenger of Allah said, "The non-virgin must not be married until she is consulted. A virgin must not be married until her permission is sought".*

Ma'ana, *"ko Mahaifi ko wani mutum wanda ke Waliyyi na wata mace ba zai aurar da ita ba ga wanda bata son ta aura. Tilas ne a samu izinin ta. Manzon Allah (SAW) ya ce, "ba za'a aurar da bazawara ba sai an shawarce ta. Kuma ba za'a aurar da budurwa ba sai an sami amincewarta."*

**Fatawar Sheik Bin Salih**

Sheik Muhammad bin Salih bin Muhammad bin Uthaimin, wanda ɗan Kwamitin Malaman Islama na Duniya ne, a ƙarkashin Hukumar Musulmi ta Duniya (World Islamic League) masu yin taro duk shekara a bisa shugabancin Sheik bin Baz a ƙasar Saudiya domin yin fatawoyi, ya yi bayani a kan mas'alar tilasta ma mata su yi aure a shafi na 244 zuwa na 246 na littafin "*Fatawa Islamiyya*". A cikin bayanan, Shehun Malamin ya ce,

*Idan Waliyyi mai darajar farko ya ƙi bayar da auren yarinya ga mutumin kirki wanda ta ke so, to sai Waliyyi mai bi masa a daraja ya bayar da ita. Idan shima ya ƙiya, to sai mai bi masa, da mai bi masa har su ƙare. Idan dukkansu suka ƙi aurar da ita ga wanda take so to sai Sarki ko Alƙali ya amshe maganar ya aurar da ita".*

**Bayanin Imam Malik**

Wannan mas'ala ta auren dole ga budurwa, Mazhabar Imam Malik ce ta zurfafa a kan ta. Hujjar kuma da Imam Malik (RA) ya

bayar a cikin littafin shi na “Muwaɗɗa”, a Babin Aure, Sashe na 28, Karamin Sashe na 2, ita ce, Malaman Madina na zamanin shi, kamar Sheik Kasim ibn Muhammad, da Sheik Salim ibn Abdullahi da Sheik Sulaiman ibn Yaser sun ce idan Uba ya aurar da ɗiyarsa budurwa ba tare da shawartarta ba, wannan aure ya yi daidai. Amma kuma a cikin wannan Sashe na 28, Imam Malik ya kawo Hadisin Annabi (SAW) kamar haka:-

Abdullah ibn Al-Fadl ya karɓo daga Nafi ibn Jubayr shi kuma ya karɓo daga Abdullah ibn Abbas, cewa Annabi (SAW) ya ce, *“Macen da ta taɓa yin aure tana da ‘yancin kanta fiye da Waliyyin ta, kuma budurwa wadda bata taɓa yin aure ba tilas ne a nemi iznin ta kamin a aurad da ita, kuma idan aka tambaye ta, sai ta yi shiru, to ta amince.”*

Idan aka auna wannan magana ta Annabi (SAW) da ta Shehunan da Imam Malik ya ambata, to ba shakka tilas a nemi iznin budurwa kamin a aurad da ita, domin maganar Annabi (SAW) ta wuce ta ko wane mutum a Duniya.

**Bayanin Littafin Askari**

Ɗaya daga cikin manyan littatafan Mazhabar Imam Malik (RA), watau *"Kitab Irshad Al-Salik*" wanda aka fi sani da "Askari" ya yi bayanai masu kyau akan wannan mas'ala ta auren tilas ta hanyar bayar da misalai daga sauran Mazhabobi. A cikin Fassara da Taƙaitaccen Sharhi a kan wannan littafi na Askari wanda Alƙali Muhammad Khalil ya yi, an bayyana a shafi na 206 cewa,

*Idan aka auna saɓanin Malamai game da wannan magana da Hadissan da suka zo a mas'alar suna nuna Uba ya shawarci 'yarsa, musamman baliga, to, wannan shi ne ya fi dacewa. Saboda shi aure a Musulunci an gina shi ne akan fahimtar juna, da kuma ƙauna da sakin rai tsakanin ma'aurata, kuma abu ne da ake fatar*

*dawwamarsa. Sharuɗɗan da Shari'ah ta shinfida na* ***kafa'a****, watau kini na namiji da mace, idan zasu yi aure ko wannensu ya duba kininsa, kuma su ga juna kafin aure, duka suna tabbatar da wannan manufa. Tunda dai akwai Hadissai ingantattu da suka zo suna nuna a shawarci budurwa da bazawara, yin haka ya fi zama maslaha a wannan zamani".*

**Faɗakarwa Ga Masu Niyyar Aure**

Ya kamata a lura da cewa Annabi (SAW) ya yi umurnin a nemi yardar budurwa ko bazawara kamin a yi mata aure domin tabbatar da cewa mijin da matar suna son juna kuma sun yi niyyar zaman aure kamar yadda Musulunci ya shimfida. Amma fa haƙƙin iyaye ko masu kula da wadda za'a aurar ne su tabbatar da cewa wanda zai aure ta ya cika ka'idojin da Musulunci ya gindaya, haka kuma masu wakiltar wanda zai yi auren su ma tilas su tabbatar da cewa wadda za'a aura ta cika waɗannan ƙa'idoji. Kamin a yi aure, ya kamata a lura da cewa:-

1. Ba kyawon huska ko dukiyar mai son yin auren ko wadda za'a aura ne abin dubawa ba. A'a, imani, ɗabi'u na gari, mutunci da rikon addinin Islama su ne abubuwan da ya kamata su zamo shika-shikan yin aure. A nan ne ake zaton samun zuri'a ɗayyiba. Hadisin da Imam Tirmizhi ya ruwaito a cikin Littafinshi "*Sunan Tirmizhi*" daga Abi Haatim Al-muzhanni, ya nuna babban abin kulawa ga wanda yazo neman aure shi ne, Addini da ɗabi'u na gari, kamar yadda Manzon Allah (SAW) ya ce,

**إِذَا جَاءَكُمْ مَنْ تَرْضَوْنَ دِينَهُ وَخُلُقَهُ فَأَنْكِحُوهُ إِلاَّ تَفْعَلُوا تَكُنْ فِتْنَةٌ فِى الأَرْضِ وَفَسَادٌ**

*Idan wanda ya zo neman auren ɗiyarku, kuka yarda da addininshi da ɗabi'unshi, to, ku aura mashi, idan baku aikata ba, fitina da ɓarna mai yawa zasu afku a bayan ƙasa.*

Dangane da macen da ya kamata namiji ya aura, Imam Al-Bukhari da Imam Muslim sun ruwaito Hadisi daga Abu Hurairah, Manzon Allah (SAW) ya ce,

**تُنْكَحُ الْمَرْأَةُ لأَرْبَعٍ لِمَالِهَا وَلِحَسَبِهَا وَجَمَالِهَا وَلِدِينِهَا ، فَاظْفَرْ بِذَاتِ الدِّينِ تَرِبَتْ يَدَاكَ**

*Ana iya auren mace saboda abubuwa guda huɗu: dukiyarta, da danganenta (watau ɗiyar wani babban mutum; mai kuɗi ko mai mulki), da kyawonta da kuma addininta, ka zaɓi ma'abuciyar addini, idan ba haka ba, to, hannuwanka za su yi ƙasa.*

2. Soyayya, haƙuri, gaskiya da riƙon amana tsakanin masu son yin aure su ne matakan dubawa na gaba. A nan ne ake zaton samun zaman lafiya tsakanin ma'aurata.Musulunci ya haramta yawancin bincike-bincike, amma ya halatta yin bincike a kan masu niyyar yin aure domin guje ma auren mata ko miji wanda bai dace ba a Shari'ance. Lallai a binciki halayen masu niyyar yin aure domin a tabbatar da cewa mutane ne na gari ba na banza ba. A nan iyaye da sauran magabata suna da damar bayar da shawara ga mai son yin aure ko wadda ake son a aura game da halayen ko wane ɗayan su. Idan mai neman auren yana da illoli to ya wajaba a yi ma wadda ake son aura huɗuba kan wannan. Ayoyin al-Kur'ani da Hadissan Manzon Allah (SAW) da bayanan Malamai sun zo da hukunce-hukunce a kan tabbatar da ingancin ma'aurata kamin a yi auren. A nan ne iyaye da Hukuma ke da ikon hana aure idan an tabbatar ɗaya daga cikin masu son yin auren bai cika ƙa'idojin aure ba. Misali, idan namiji mai son ya auri yarinya an gano cewa kafiri ne ko kuma babban fasiƙi ne mai yawaita aikata manyan zunubbai kuma babu alamar zai yi nadama ko ya tuba, to, a nan komin son da yarinya ta ke yi ma sa, bai halatta ba a ƙyale ta, ta aure shi. Wannan hukuncin kuma ya shafi namiji kamar yadda ya shafi mace.

# Babi Na Ukku
# WALICCI WAJEN YIN AURE

Ruɗani a kan wane ne ya fi dacewa ya zama Wali a wajen aure, shi ma yana ci ma Musulmi tuwo a ƙwarya. Domin Walicci shi ne ke tabbatar da aure na gari ko kuma ɓatacce. Kuma Wali shi ke jagoranci wajen yi ko hana auren dole. Wali (ko Waliyyi), watau wanda zai bayar da mace zuwa ga mijin ta lokacin ɗaura aure, yana ɗaya daga cikin manyan sharuɗɗan aure, sauran sune, sadaki (kuɗin da za'a ba matar da za'a aura), da siga (yadda ake ɗaura aure) da jama'a masu shaida.

Annabi Muhammad (SAW) ya yi bayani a kan muhimmancin Wali inda Hadisi na 2080 na Sunan Abu Dawood ya ruwaito Abu Musa yana cewa, Annabi (SAW) ya ce, **لاَ نِكَاحَ إِلاَّ بِوَلِيٍّ**"*Babu aure sai da Wali.*" Kuma Ahmad da Tirmidhi sun ruwaito cewa Annabi (SAW) ya ce, "*Idan mace ta yi aure ba tare da Wali ba, to babu auren, babu auren, babu auren.*"

Al'adu da ɗabi'u, musamman a ƙasar Hausa sun tauye tsarin walicci da Shari'ah ta shinfiɗa. Waɗanda Shari'ah ta fifita an maye su da waɗanda al'adu da ɗabi'u suka fifita. Wannan babban kuskure ne wanda tilas a gyara shi ko kuma aure ya ɓaci, watau ya koma waɗanda ake gani kamar "ma'aurata" su koma "mazinata", wa iyazu bil Lahi!

## JERIN MASU WALICCI

Dukkan Mazhabobi da Malamai sun yi ittifaƙi da cewa tilas ne a samu Wali da zai bayar da mace wajen aure kamin auren ya inganta, idan ba haka ba to, auren ya haramta.

Sheik Abubakar ibn Asim al-Garnadi al-Andulusi ya rubuta littafi a kan Shari'ar Musulunci mai suna "*Tuhufatul Hukkam.*"

Sheikhibn Asim ya wallafa littafin ne a shekarar 820 Hijrah (watau fiye da shekaru 600 da suka wuce) kuma har yanzu ana taƙama da shi. A tarjamar littafin da marigayi Alƙalin Alƙalan Jihar Katsina, Sheik Usman Muhammad Daura ya yi, da sunan "Jagorar Masu Hukunci", an bayyana sifofin da Wali tilas ya same su, a Baiti na 346, shafi na 152, kamar haka:-

1. Ɗa (watau ba bawa ba)
2. Baligi (cikakken wanda ya balaga)
3. Mai hankali (ba mahaukaci ko ruɗaɗɗe ba)
4. Namiji (ba mace ba)
5. Wanda bai ɗaura haramin aikin Hajji ko na Umrah ba
6. Musulmi, idan wadda za'a aurar Musulma ce

Sannan akwai wasu sifofin waɗanda wasu malamai suka ce ba tilas bane Wali ya same su, watau:-

1. Shiryayye wanda ya san sharuɗɗan aure
2. Adali (wanda zai zaɓi mijin kirki ba da son ran shi ba)

Bayan cika ƙa'idojin waɗannan sifofi sai maganar shin wane ne a kan gaba wajen zama Wali? Watau, wane ne ke da darajar farko da ta biyu da ta ukku da dai sauransu, waɗanda idan aka taru wajen ɗaura aure, to tilas a ce wane ne yafi sauran iko sannan sai wane, sai kuma wane. To, a nan ne gizo ke saƙa a cikin al'adun Hausawa. Waɗanda al'ada ta gabatar ba su ne Shari'ah ta sanya a jerin gaba ba. Misali kullum an ɗauka cewa wan-Uban yarinya (musamman idan Uban ya mutu) shi ne kan gaba sannan sai ƙanen-Uba, sannan sai wasu, kuma ba'a ma maganar ɗan-uwan yarinyar. To ba haka bane a Shari'ah.

**Idan cikakkar mace ce, wadda ta taɓa yin aure har ta haifi ɗa wanda ya balaga ko 'ya'ya maza waɗanda suka balaga,** to, ga

jerin wanɗanda Shari'ah ta yarda da su, kuma a kan wane na gaba da wane, watau na ɗaya a wannan jeri shi ne na ɗaya a muhimmanci, sannan sai mai bi masa sannan mai bi masa. Baiti na 348 na *Tufhatul Hukkam*, shafi na 152 ya jeranta Waliyyai a kan irin wannan mace da aka ambata, kamar haka:-

1. Ɗanta (namiji, baligi)
2. Mahaifinta (Uba)
3. Ɗan-uwanta shaƙiƙi
4. Ɗan-uwanta li-abbi
5. Kaka (mahaifin Uba)
6. Baffa (ɗan-uwan uba) shaƙiƙi
7. Baffa (ɗan-uwan uba) li-abbi
8. Wanda ya rene ta
9. Hukuma (Sarki ko Alƙali)

A lura cewa an fara gabatar da ɗan ita matar kafin mahaifinta a nan kamar yadda yake a wajen gado, domin shi mahaifi yana cin gado da farilla, amma shi ɗa "*asibi*" ne, watau wanda ke kwashe sauran dukiya duka. Saboda haka, tun da ɗa ya fi karfi wajen gado, to, shi yasa ya fi karfi a wajen Walicci. Kuma Malamai sun bayyana cewa, ɗa - wanda ke saurayi kuma ya balaga ya fi damuwa da kishin irin mutumen da uwarsa zata aura fiye da mahaifin ita matar wanda ba shakka tsoho ne a wannan marra don haka damuwarsa ba zata kai ta saurayin ɗanta baligi ba.

**Idan mace ce, wadda ba ta taba aure ba (watau budurwa),** to, ga jerin wanɗanda Shari'ah ta yarda da su (daga *Tuhfatul Hukkam*) kuma a kan wane na gaba da wane, watau na ɗaya a wannan jeri shi ne na ɗaya a muhimmanci, sannan mai bi masa, sannan mai bi masa:-

1. Mahaifinta (Uba)
2. Ɗan-uwanta shaƙiƙi
3. Ɗan-uwanta li-abbi
4. Kaka (mahaifin Uba)
5. Baffa (ɗan-uwan uba) shaƙiƙi
6. Baffa (ɗan-uwan uba) li-abbi
7. Wanda ya rene ta
8. Hukuma (Sarki ko Alƙali)

**Idan ko marainiya ce budurwa (watau wadda mahaifinta ya mutu)**, Sheik Abdulaziz bin AbdulLah bin AbdulRahman al-Baz wanda aka fi sani da Sheik bin Baz, ya bayar da fatawa a kan wanda zai mata Walicci. Sheik bin Baz ya yi bayanin jerin waɗanda zasu yi ma marainiya Walicci a cikin littafin "*Fatawa Islamiyya*", shafi na 247 zuwa na 248 kamar haka:-

1. Kakanta (mahaifin Uba)
2. Ɗan-uwanta shaƙiƙi
3. Ɗan-uwanta li-abbi
4. Ɗan Ɗan-uwanta shaƙiƙi
5. Ɗan Ɗan-uwanta li-abbi
6. Baffa (ɗan-uwan Uba) shaƙiƙi
7. Baffa (ɗan-uwan Uba) li-abbi
8. Wanda ya rene ta
9. Hukuma (Sarki ko Alƙali)

**A lura:- Hukuma (watau Sarakuna da Alƙalan Musulunci)** an jeranta su daga ƙarshe, amma kuma ikon su ya fi na suran, domin su ne za su iya rusa duk abinda wani daga cikin Waliyyan ya yi, muddin dai abinda ya yi ya saɓa ma Shariah.

Ya kamata kuma a fahimci cewa, mafiya rinjayen Malaman Duniya sun yarda da tsare-tsaren Walicci, kwatankwacin wanɗanda aka bayyana a sama. Kuma ko wane Waliyyi yana da ikon naɗa wakili kuma idan Uba ya yi wasicci, to wanda ya wasitta zai wakilce shi amma a matsayin da Uban ya ke ba wai ya haye matsayin wani ba.

Ba shakka za'a yi mamakin tsarin da ya gabatar da ɗa wanda mace ta haifa da cikinta a kan mahaifinta, ko kuma ɗan-uwanta wanda suka fito ciki ɗaya a kan baffanta (watau wa ko ƙanen mahaifinta) da dai sauransu. To, haka dai Shari'ah ta yi tsarin, kuma al-ada ko ɗabi'a ko son zuciya basu iya kauda wannan. Hattara ta wajaba akan Musulmi a kan wannan al-amari domin tilas a bi yadda Allah (SWT) da Annabi Muhammad (SAW) da Sahabbai (AS) da haɗuwar Manyan Malaman Islama suka tsara a kan duk al-amurra.

# Babi Na Huɗu
# NEMA DA ƊAURA AURE

Da zarar namiji ya yi niyyar yin aure, to, sai maganar neman wadda za'a aura ta shigo. Ita ma mace, da ta isa aure sai irin wannan magana ta shigo. Sheikh Ahamad Bello Dogarawa ya bayar da shawarwari a kan neman aure a cikin littafin shi mai suna, "Tarbiyyar 'Ya 'Ya a Musulunci" kamar haka:-

**Abubuwan lura a wajen zaɓen abokiyar zama su ne:**

1. Riƙo da addini ( kamar yadda fito a Kur'ani, 2:221)
2. Sahihiyar aƙida (kamar yadda Timidhi ya ruwaito)
3. Kyawawan ɗabi'u (kamar yadda Timidhi ya ruwaito)
4. Iya soyayya (kamar yadda Ahmad da Abu Dawud su ka ruwaito)

A wajen zaɓen abokin zama, mace ta yi tarayya da namiji a cikin mafi yawan waɗannan ɗabi'u. Don haka, wajibin iyaye ne su zaɓa wa ɗiyarsu miji na ƙwarai bisa lura da waɗannan siffofi.

**Yana daga abubuwan da aka hana a cikin neman aure:**

1. Kaɗaita da wadda za'a aura, ko yin tafiya tare da ita, ko fita yawon shaƙatawa ba tare da wani muharramin ta ba, ko da kuwa an biya sadaki ( a duba ruwayar Bukhari, Muslim, Ahmad da Tirmidhi)
2. Taɓa jikin wadda za'a aura, ko rungumar ta, ko sumbantar ta, ko da an biya sadaki ( a duba ruwayar Ɗabarani).
3. Maganganun batsa a wajen hira, ko aikawa da saƙon da ke ɗauke da maganganun batsa ko hotunan tsiraici ko sakarci ko motsar da sha'awarta cikin wayar tafi-da-gidan-ka.
4. Kwanciya (jima'i) da wadda za a aura tun kafin a ɗaura auren, ko da an biya sadaki.

**Saboda muhimmancin aure** da babban tasirinsa a kan tarbiyyar ‘ya’ya, Musulunci ya ɗauki mataki na dawwamar da aure, a tsakanin miji da mata, matuƙar babu wata larurar da ta bijiro. Daga cikin hanyoyin da Musulunci ya bi domin dawwamar da aure akwai:

1. Fifita addini da kyakkyawar ɗabi’a a wajen zaɓen miji ko mata.
2. Halatta kallon wadda a ke son a aura ga wanda zai aura.
3. Sharɗanta yardar wadda za a aura.
4. Hana wa miji da mata neman kamala daga wajen junan su, da bayyanar da muhimmancin yin haƙuri da juna.
5. Halatta wa mutane shiga cikin al’amarin ma’aurata domin yin gyara da sulhu a tsakaninsu, idan akwai buƙatar yin haka.
6. Halatta yin ƙarya, wadda ba za ta cutar ba kuma ba yaudara ba, a tsakanin ma’aurata domin zamantakewa ta ƙara danƙo.
7. Wajabta wa ma’aurata zamantakewa kyakkyawa a tsakanin su, ta hanyar bayyana wa kowannensu haƙƙoƙin sa, da kuma haƙƙoƙin da ke kansa.

Bayan namiji da mace sun daidaita a tsakanin su cewa zasu yi aure, sai maganar ɗaura aure ta shigo. A nan ne za’a duba muhimman sharuɗɗa guda huɗu, waɗanda idan ba a cika su ba duka, to, babu aure ke nan. Watau tilas ne a tabbatar da cika dukkan waɗannan sharuɗɗa guda huɗu kamin aure ya inganta. Ga waɗannan sharuɗɗa:-

**1. Waliyyi**

Wali (ko Waliyyi) shi ne sharaɗi na farko. An riga an yi cikakken bayani a kan shi a Babi na Goma Sha Biyu.

**2. Sadaki**

Sadaki shi ne sharaɗi  na biyu wanda idan babu shi, to babu aure. Sadaki na nufin wani abu mai daraja kamar kuɗi ko wata ƙaddara ko makamantan waɗannan da za’a ba mace a matsayin haƙƙin ta na aure. A Mazahabar Malikiyya an shar’anta cewa darajar abin da za’a bayar a matsayin Sadaki mafi ƙaranci shi ne, ɗaya-bisa-huɗu na darajar Dinari (watau rub’u Dinar ko ¼ Dinar) daga nan abin da ya yi sama, babu iyaka. A ko wace ƙasar duniya ana kwatanta darajar kuɗin ƙasar da na Dinari, sannan a ƙiyasta ko nawa za’a biya a matsayin Sadaki. Allah (SWT) Ya faɗa a cikin al-Kur’ani, Sura ta 4, Aya ta 4:-

وَءَاتُواْ ٱلنِّسَآءَ صَدُقَٰتِهِنَّ نِحۡلَةٗۚ فَإِن طِبۡنَ لَكُمۡ عَن شَيۡءٖ مِّنۡهُ نَفۡسٗا فَكُلُوهُ هَنِيٓـٔٗا مَّرِيٓـٔٗا

*(tilas) Ku ba mata Sadakin su da zuciya kyakkyawa. Amma idan (bayan kun ba su) sai su ka baku wani abu daga cikin sa cikin daɗin rai, to, sai ku (amsa) ku ci cikin daɗin rai.*

Bukhari da Muslim sun ruwaito Manzon Allah (SAW) ya ce,

**« انظر ولو خاتم من حديد ».**

*Ku samo abinda zaku ba matayen ku, ko da zoben ƙarfe ne.*

Musulunci yana son a sauƙaƙawa wajen aure. Ahmad da Al-Hakim da Baihaki sun ruwaito Manzon Allah (SAW) yana cewa,

**« إِنَّ أَعْظَمَ النِّكَاحِ بَرَكَةً أَيْسَرُهُ مُؤْنَةً ».**

*Auren da yafi albarka, shi ne, na mata wadda ta fi sauƙi wajen kulawa da ita.*

### 3. Shaidu

Samun shaidu wajen ɗaura aure shi ne sharadi na ukku. Tilas ne a samu shaidu aƙalla guda biyu waɗanda zasu shaida cewa an ɗaura ma wane aure da wance. Watau bayan mai neman aure (ko wakilin shi) da mai bayarwa (Wali), tilas ne wasu mutane daban su biyu su shaida ɗaurin auren. Kamar yadda Allah Ya shar’anta a tsaida shaidu biyu wurin sakin aure, to, haka ma wajen ɗaura aure tilas a samu aƙalla shaidu biyu kamar yadda Allah ke cewa:

وَأَشۡهِدُواْ ذَوَىۡ عَدۡلٖ مِّنكُمۡ

*Kuma ku sanya mutane adilai guda biyu daga cikin ku, domin su yi maku shaida* (Al Talaƙ: 2)

Tirmizhi da Baihaki sun ruwaito cew Annabi (SAW) ya ce,

«لاَ نِكَاحَ إِلاَّ بِوَلِيٍّ وَشَاهِدَىْ عَدْلٍ».

*Babu aure idan babu Wali da shaidu adilai guda biyu.*

Abin fahimta a nan shine, a ƙalla a samu shaidu adilai guda biyu, idan aka samu fiye da guda biyu, har suka kai milyan guda ko ma fiye da haka, aure ya yi. Kuma shaidun nan tilas su zama mazaje ne kuma adilai. Sheik Abu Bakr Jabir Al-Jaza'iry ya yi bayani a Babin Aure a cikin littafin sa na *Minhaj Al-Muslim*, cewa, adilai a nan ana nufin waɗanda basu aikata manyan zunubbai kuma suna guje ma ƙananan zunubbai. Watau mutumin da ke zina, ko shan giya ko zamba, ba za'a karɓi shaidar sa ba. Don haka, ba zai yiwu a sanya irin waɗannan mutanen ba cikin shaidu adilai guda biyu da aka ambata. Lallai a kula da wannan Magana domin tana iya gyara ko ɓata aure.

**4. Sigar Ɗaura Aure**

Sharaɗi na huɗu, kuma na ƙarshe, shi ne, Sigar Ɗaura Aure, watau yadda ake tafiyar da ɗaura auren gaban shaidu. Mai neman aure yana iya zuwa ya karɓi auren da kansa ko kuma ya naɗa Wakili, amma ita matar da za'a auras, Waliyyinta ne ke da ikon bayar da auren ta. Ga misalin Sigar Aure:-

Mai neman aure zai ce, *"ina neman auren wance daga gareka".* Shi Walliyin ta sai ya ce, *"na baka auren wance".* Mai neman aure sai ya ce, *"na karɓi auren wance bisa ga zimmar auren*".

Daga nan an so a yi huɗubar cewa, daga wannan lokaci abinci, da abin sha, da sutura, da muhalli, da koyar da addini da abububuwa

makamantan waɗannan sun tashi daga kan masu renon yarinyar ko matar sun koma kan mijinta.

Kuma anso a yi addu'oi domin samun albarka a cikin auren da fatar Allah Ya bayar da zuri'a mai albarka. Yana da kyau a nan a ƙara da yin addu'oin samun gafara ga iyaye da sauran magabata da kuma samun lafiya da zama lafiya ga al'ummah baki ɗaya.

**Matashiya:-** Wanda zai bayar da mace wajen ɗaurin aure (watau Amarya wadda za'a aura) shi ake kira "Waliyyi". Kuma shi namijin da zai yi aure (watau Ango) yana iya zuwa ya karɓi auren da kan shi ko kuma ya naɗa "Wakili". Abin lura a nan shi ne, na wajen namiji mai yin aure sunan shi "Wakili" na wajen macen da za'a aura kuma sunan shi "Waliyyi". Watau ba'a kiran na wajen Ango da sunan "Waliyyi" kuma ba'a kiran na wajen Amarya da sunan "Wakili". Kuma Ango na iya zuwa da kan shi ya amshi auren amma ita Amarya bata iya zuwa ta bayar da kanta.

# HAKKOKIN MA'AURATA

Babi na Ɗaya na wannan littafi ya yi cikakken bayani a kan muhimmancin yin aure. A cikin wancan Babin, an kawo Faɗar Allah (SWT) da faɗar Manzon Allah (SAW) waɗanda suka tabbatar da muhimmancin yin aure a cikin Musulunci. Ba shakka, aure Sunnah ne, amma da an yi niyyar yin shi, har zuwa tarewar matar gidan mijinta, har zuwa tsawon rayuwarsu a duniya, sai Wajibai su shigo waɗanda karya su zai jaza manyan zunubbai da hukunce-hukunce.

Wani gagarumin al-amari shi ne a yi la'akkari da cewa, a cikin Musulunci mutane basu yaɗuwa, watau ba'a haihuwa, sai da aure. Ashe idan babu aure to sai wata rana a tashi babu Musulmi ko ɗaya domin Musulunci bai yarda da samun 'ya'ya ta hanyar zina ba. Kuma a lura da cewa a cikin al-Kur'ani Allah (SWT) cewa Ya yi Ya halitta ma Annabi Adam (AS) **"matar aure"** Hawwa'u (RA) (watau وخلق منها زوجها) ba cewa Ya yi ba **mace kawai** (watau المرأة).

Sannan a lura da cewa, Annabi (SAW) ya ce yana yin **aure** kuma aure Sunnah ne, kuma wanda duk ya ƙyamaci Sunnar sa to baya tare da shi. Kuma Annabi (SAW) ya umurci matasa su yi aure muddin suna da halin yi. Sannan Annabi (SAW) ya ce yana so Musulmi su yi aure kuma su hayayyafa domin ya yi alfahari da cewa al-ummar sa ta fi ta kowa yawa a lahira.

Idan aka duba waɗannan dalillai, ana iya cewa aure tilas ne ga duk Musulmin da ya cika ƙa'idojin yin sa. Domin idan babu aure ashe wata rana babu sauran Musulmi 'yan halas sai dai 'yan zina, Allah Ya sauwaƙe, ameen.

To, da anyi aure sai kuma haƙƙoƙin ma'auratan biyu su shigo, watau haƙƙoƙin miji da na matar sa. Waɗannan haƙƙoƙin suna

da yawan gaske amma ga muhimmai daga cikin su kamar yadda Sheikh Ahmad Bello Dogarawa ya bayyana a littafin shi mai suna "Tarbiyyar 'Ya 'Ya a Musulunci:-

**Haƙƙoƙin ma'aurata** kashi ukku ne, watau (1) waɗanda suka yi tarayya a kai; (2) waɗanda mata ta ke da su a kan mijinta; da (3) waɗanda miji ke da su a kan matar shi.

**HAKKOKIN DA SUKA YI TARAYYA** a kai guda ukku ne:-

1. Haƙƙin jima'i da jin daɗin juna (Suratun Nisã, 4:20-21; Suratul Baƙarah, 2:223; Bukhari)
2. Haƙƙin gadon dukiyar wanda ya riga mutuwa (Suratul Nisã, 4:11-12)
3. Haƙƙin dangantuwar 'ya'ya (Bukhari da Muslim)

**HAKKOKIN MATA A KAN MIJINTA** sun haɗa da:

1. Biyan sadaki (Suratun Nisã, 4:4).
2. Ɗaukar nauyi da ɗawainiya; da ciyarwa da tufatarwa; da kula da lafiya; da bayar da muhalli (Suratul Baƙarah, 2:223; Suratun Nisã, 4:34).
3. Kyakkyawar mu'amala (Suratun Nisã, 4:19).
4. Jima'i, gwargwadon ikon shi da yanayin shi (Bukhari da Muslim)
5. Rashin marin fuska da bugu mai cutarwa (Suratun Nisã, 4:34; Bukhari).
6. Kiyaye sirrin jima'i (Abu Dawud).
7. Adalci a tsakanin kishiyoyi (Suratun Nisã, 4:129; Abu Dawud).
8. Karantar da addini (Suratut Tahrim, 66:6; Bukhari).
9. Tsare mutunci da rashin cin mutunci (Bukhari da Muslim).
10. Rashin watsarwa ko wofintarwa (Ahmad da Muslim).

**HAKKOKIN MIJI A KAN MATARSA** sun haɗa da:

1. Samar mashi da sukuni da natsuwa a cikin gida (Suratul A'arãf, 7:189; Suratur Rum, 30:21).
2. Yarda da shugabancin shi ga gida (Suratun Nisã, 4:34)
3. Yi mashi biyayya a duk abin da bai saɓa ma Allah ba (Hakim).
4. Biya mashi buƙatar jima'i, matuƙar babu larurar da za ta hana (Tirmidhi).
5. Rashin barin wani mutum ya shiga gidan, muddin bashi so (Bukhari da Muslim).
6. Rashin fita daga gida ba tare da izinin shi ba (Suratul Ahzãb, 33:33).
7. Yi mashi dukkan nau'o'in hidima, gwargwadon iko, kuma gwargwadon *urf*, watau al-adar da bata saɓa da Shari'ah ba. (Ahmad, Bukhari da Muslim).
8. Taimaka mashi da nuna mashi goyon baya da ƙarfafa gwuiwa a cikin dukkan abubuwan da Shari'ah ba ta hana ba (An-Nasã'i)
9. Gode ma ƙoƙarin shi, da rashin matsawa a kan buƙatun da babu tilas ko larura a cikin su (Bukhari, Muslim, An-Nisã'i, Hãkim).
10. Rashin yin azumin nafila ba tare da izinin shi ba, muddin bai yi tafiya ba (Bukhari da Muslim).

# Babi Na Shidda

# WASU MUHIMMAN MAS’ALOLI

## SAI MAI HALIN YIN AURE NE ZAI YI AURE?

Idan aka duba haƙƙoƙin mata a kan mazajen su, musamman manyan haƙƙoƙin ciyarwa, da tufatarwa, da bayar da muhalli, da koya addini, da kula da lafiya da biyan sauran buƙatun yau-da-kullum, za’a yi tambaya cewa, “shin sai mai halin biyan waɗannan buƙatu ne zai yi aure?” Wajen bayar da amsar wannan tambaya tilas a lura da cewa.

1. Allah (SWT) Ya faɗa a wurare da yawa a cikin Al-Kur’ani cewa bai aza ma wata rai abin da bata iya wa ba. Don haka idan mutum ya yi abinda ya ke iyawa na aikin lada Allah zai biya shi da lada (watau al-Jannah), kuma idan mutum ya yi abin da ya ke iyawa na aikin zunubi shi ma Allah zai biya shi da zunubi (watau wuta). Ga misalin ɗaya daga cikin Ayoyi da dama na Al-Kur’ani inda Allah Ya ke magana a kan iyawa ko gajiyawar ɗan-Adam.

لَا يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَا ۚ لَهَا مَا كَسَبَتْ وَعَلَيْهَا مَا ٱكْتَسَبَتْ ۗ

*Allah ba Ya ɗora ma wata rai (ɗan-Adam) (wani abu) sai gwargwadon ikon ta, tana da ladar abin da ta aikata (na alheri), kuma (azabar) abin da ta aikata (na sharri) ya na kan ta.* (Suratul Baƙara, 2:286)

2. Allah (SWT) cikin Rahamar Shi, yana ɗauke ma mutum yin Azumi, da Hajji da Zakka da duk sauran ayyukan farillu da wajibai muddin dai mutumin ba ya iya aikata su (kamar wanda tsananin tsufa ya hana shi azumi) ko kuma bai da halin zuwa ya aikata su (kamar wanda bai da halin zuwa aikin Hajji).

Watau idan mutum zai yi wani abu, to, Allah Ya ba shi damar yin abin gwargwadon ikon shi ke nan. Misali, mai iya yin tsayuwar

Sallah sai ya yi Sallah da ga tsaye, wanda ba ya iyawa sai ya yi daga zaune. Kuma wanda yunwa zata halaka shi idan naman Alade ne kaɗai ya iya samu sai ya ci. Sabo da haka, kowa sai ya yi ƙoƙari ya auro mata dai-dai da shi wadda halin samun shi zai iya kula da ita da iyalin da Allah zai iya ba su. Idan kwata-kwata mutum bai da halin iya yin aure, to ga abin da Allah Ya ce,

وَمَن لَّمۡ يَسۡتَطِعۡ مِنكُمۡ طَوۡلًا أَن يَنكِحَ ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ فَمِن مَّا مَلَكَتۡ ـكُم

بِإِيمَٰنِكُم أَعۡلَمُ وَٱللَّهُ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ فَتَيَٰتِكُمُ مِّن أَيۡمَٰنـ...

ذَٰلِكَ لِمَنۡ خَشِيَ ٱلۡعَنَتَ مِنكُمۡۚ وَأَن تَصۡبِرُواْ خَيۡرٞ لَّكُمۡۗ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ

*Wanda bai sami wadatar da zai auri 'ya'ya muminai daga cikin ku ba, to, sai (ya aura) daga abin da hannuwanku suka mallaka daga bayin ku muminai. Allah Shi ne mafi sanin imanin ku … Wannan (izni na auren baiwa) ga wanda ya ke tsoron faɗawa cikin ɓarna ne daga cikin ku. Idan kuka yi haƙuri, shi ya fi alheri a gare ku. Allah kuma mai Gafara ne, mai Rahama ne.* (Suratun Nisa, 4:25)

Kuma Allah (SWT) Ya ce,

فَضۡلِهِۦ مِن ٱللَّهُ يُغۡنِيَهُمُ حَتَّىٰ نِكَاحًا يَجِدُونَ لَا ٱلَّذِينَ وَلۡيَسۡتَعۡفِفِ

*Waɗannan waɗanda ba su da halin yin aure, su kame kawunan su (da tsarki) har lokacin da Allah Ya basu hali daga cikin falalar shi.* (Suratun Nuur, 24:33)

Manzon Allah (SAW) ya yi bayanai da yawa a kan abubuwan da waɗanda ba su da halin aure za su yi, kamar yawaita yin azumi, da zikirin Allah domin sha'awar mata ta gushe daga gare su.

Bukhari da Muslim sun ruwaito cewa, wata rana Annabi (SAW) ya ga wasu matasa maza, Musulmi, wasun su suna zaune suna hira kuma wasun su suna wasanni, sai ya ce ma su, "*Ya ku*

*wannan rukunin matasa! Wanda duk ke da hali a cikin ku, to, ya yi aure".*

Watau kalmomin da za'a lura da su a nan su ne, **"wanda duk ke da hali a cikin ku, to, ya yi aure".** Ashe sai da halin **ɗaukar nauyin haƙƙoƙin** ba mata muhalli, abinci, abin sha, sutura, koyar da addini da sauran haƙƙoƙi makamantan su ake iya yin aure.

Waɗannan haƙƙoƙi na mata suna kawo ruɗani a wannan zamani don haka za'a yi ƙoƙarin bayyana su gwargwadon yadda Allah (SWT) Ya sanar daga cikin ilmin Shi domin Shi ne ke da sanin duk abin da ke bayyane da na ɓoye.

## WANE IRIN GIDA NE ZA'A SANYA MATAR AURE?

Littafin ***Sahihu Fiƙhus Sunnah*** na Abu Malik Kamal bin Sayyid Salim, Juz'i na 3, Shafi na 198 zuwa na 204 ya yi bayanai da suka shafi wurin zaunar da matar aure, watau muhalli. Littafinya bayyana cewa irin gidan da ya dace a sanya matar ko matan aure shi ne wurin zama wanda mace zata amintu ga kanta da dukiyar ta, wurin da zai suturta ta daga idanun jama'a, kuma ya bata damar samun jin daɗin zaman aure da mijinta, ba tare da matsi ko makamancin haka ba, watau ba gidan da zai cutar da ita ba.

Mafi yawan malamai suna ganin cewa wadatar miji ce abin yin la'akkari, ba halin mace ba, watau shin mawadaci ne, ko kuwa talaka ne? A nan, malamai sun dogara ne da faɗar Allah (SWT) a cikin Suratuɗ Ɗalaƙ, Aya ta 6:-

أَسۡكِنُوهُنَّ مِنۡ حَيۡثُ سَكَنتُم مِّن وُجۡدِكُمۡ

*ku zaunar da su inda kuke zaune, gwargwadon samunku*

Ga yadda bayanin wannan ayar al-Kur'ani ta zo a cikin Littafin ***Sahihu Fiƙhus Sunnah,*** Juz'i na 3, Shafi na 202:-

**صفة المسكن الشرعى: المعتبر فى المسكن الشرعي للزوجة هو سعة الزوج وحال الزوجة، قياسا على النفقة باعتبار أن كلاً منهما حق مترتب على عقد الزواج.**
**فالواجب يكون بقدر حال المنفقة يسرا وعسرا وتوسطا، فكذلك السكنى، وهو مذهب الجمهور.**

*Siffar wurin zama a Shari'ah:- Abin lura wajen bada wurin zama ga mace a Shari'ah shi ne wadatar mijin da kuma halin matar (ko matsayinta), watau in an kwatanta da ciyarwa (don shi ma haka hukuncin ya ke), da ciyarwa da wurin zama haƙƙi ne abin lura tun wajen ɗaura aure.*

*Abinda ke wajibi dai shi ne:- gwargwadon halin mai badawa – wadata ko talauci ko tsaka-tsaki. To haka abin yake wajen bada wurin zama, wannan shi ne Mazhabar mafi yawan Malamai.*

Amma malaman Mazhabar **Shafi'iyya** sun ce matsayin mace ake dubawa wajen wurin zama, ba na mijin ta ba, don suna ganin mace dole ta zauna a wuri irin wanda ta saba da shi, in ba haka ba, to an cutar da ita. Ga yadda bayanin wannan fahimta ta zo a cikin Littafin ***Sahihu Fiƙhus Sunnah***, Juz'i na 3, Shafi na 203:-

**وقال الشافعية: المعتبر فى المسكن الشرعى هو حال الزوجة فقط على خلاف قولهم فى النفقة. قالوا؛ لأن الزوجة ملتزمة بملازمة السكن، فلا يمكنها إبدا بها، فإذا لم يعتبر حالها فذلك إضرار بها، والضرر منهى عنه شرعا، أما النفقة فيمكنها إبدالها.**

*Shafi'iyya suka ce:- abin kulawa dai wajen ba da wurin zama a Shari'ah shi ne:- hali ko matsayin matar kaɗai, "saɓanin abinda suka ce wajen ciyarwa". Sun ce; abinda ya zama tilas ga mace shi neta zauna wuri irin wanda ta saba da shi, bai kamata a canza mata ba, idan ba'a kula da matsayin ta ba, to an cutar da ita, Shari'ah kuwa ta hana a cutar da ita. Amma abinci ta iya canzawa ko a canza mata.*

## ANA IYA HAƊA MATAN AURE BIYU, UKKU KO HUƊU A CIKIN GIDA ƊAYA?

Littafin ***Sahihu Fiƙhus Sunnah,*** Juz'i na 3, Shafi na 198 zuwa na 204 ya yi bayanai a kan wannan mas'ala. Littafin ya bayyana cewa, yawancin malamai suna ganin cewa ba'a haɗa mace ko mata da wasu 'ya 'yan miji ko iyayen shi ko kuma 'yan uwan-shi don su zauna tare a gida ɗaya, sai fa idan ita ce ta zaɓi haka, domin wurin zama haƙƙin ta ne, ba dole ne tayi tarayya da wani ba, domin akwai cutarwa a gare ta, musamman wajen zamantakewar aure.

Juz'i na 3, Shafi na 204 na littafin **Sahihu Fiƙhus Sunnah** ya ƙara bayani kamar haka:-

**فذهب الجمهور (الحنفية والشافعية والحنابلة) إلى أنه لا يجوز الجمع بين الأبوين (أو غيرهما من الأقارب) والزوجة فى مسكن واحد. ويكون للزوجة الامتناع عن السكنى مع واحد منهما إلا أن تحت رهى ذلك. لأن السكنى من حقها فليس له أن يُشرك غيرها فيه. ولأنها تتضرر بذلك.**

*Haɗuwar Malamai na Mazhabar Hanafiyya, Shafi'iyya da Hambaliyya sun tafi akan cewa:- bai halatta a haɗa mace da iyayen miji ko wasun-su su zauna tare a gida ɗaya ba, sai da izinin-ta, ganin damar ta ne, ta zauna da su, domin wurin zama haƙƙinta ne, babu damar a haɗa ta zama da wani, domin yin hakan zai iya cutar da ita.*

Kuma haka hukuncin yake wajen ita macen, idan tana so ta zauna da nata dangin a gidan miji, hakan ba zai samu ba, sai in ya amince, in bai amince ba, to dole ta maida su gidan su, domin zama da dangin ta a gidan mijinta ba haƙƙin ta ba ne, na mijin ne, sai in ya yarda.

Maganar haɗa mace fiye da ɗaya kuwa, watau biyu ko ukku ko kuma huɗu a gida ɗaya, malamai sun haɗu kan cewa haɗa su a

gida ɗaya (ɗakin wannan na kallon na waccan) bai halatta ba, domin babu abinda ake kira da Larabci, المعاشرة بالمعروف watau kyakkyawan zama na jin daɗin zaman aure. Irin wannan haɗawar kuma tana haddasa husuma tsakanin mata, ga shi Shari'ah ta yi hani da haka.Sannan, zai yiwu gudar matar ta ji tana buƙatar mijinta a lokacin da taga ko taji alamun ya je wajen ɗayar. Wannan zai jawo gaba da kishi a tsakanin su, sabo da haka aka hana a haɗa mata biyu a gida ɗaya. Wannan haƙƙin su ne, amma a ra'ayin mafi yawan malamai haƙƙin yana saraya idan sun yarda su zauna tare a gida guda; sai dai ya fi kyau a raba su domin ko sun yarda, fitina ta kan taso a-kai-a-kai.

**Watau wajibi ne a ba ko wace matar aure gidan ta daban ko aƙalla a keɓe mata shiyyar ta daban yadda wannan matar ba ta ganin ko jin abinda ɗayar ta ke yi ko ta ke ciki.**

A Mazhabar **Malikiyya** kuma, an ce ana iya banbanta tsakanin mace da ta fito daga babban gida, kamar 'yar Sarki ko Attajiri ko Malami da wadda ba irin wannan mace ba. Watau ba'a haɗa mace da ta fito daga babban gida da kowa, kamar wata matar auren ko iyayen miji ko 'ya'yan shi ko makamantan waɗannan. Amma idan ba daga babban gida ta fito ba, to ba laifi idan an haɗa ta da wasu, in babu cutarwa gare ta, kuma idan akwai cutarwa, to ita ma ba'a haɗa ta da kowa.

Waɗannan bayanai na cewa ko wace mace a keɓe mata gidan kanta, sun samo asali ne daga yadda Annabi Muhammadu (SAW) ya yi. Za'a iya fahimtar haka daga Alƙur'ani mai Girma, inda Allah (SWT) Ya ce, a cikin Suratul Ahzab Aya ta 32 da ta 33:-

يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِيِّ لَسۡتُنَّ كَأَحَدٖ مِّنَ ٱلنِّسَآءِ إِنِ ٱتَّقَيۡتُنَّ فَلَا تَخۡضَعۡنَ بِٱلۡقَوۡلِ فَيَطۡمَعَ ٱلَّذِي
فِي قَلۡبِهِۦ مَرَضٞ وَقُلۡنَ قَوۡلٗا مَّعۡرُوفٗا ٣٢ وَقَرۡنَ فِي بُيُوتِكُنَّ وَلَا تَبَرَّجۡنَ تَبَرُّجَ ٱلۡجَٰهِلِيَّةِ
ٱلۡأُولَىٰ

*Ya ku matan Annabi, ba ku zamo kamar sauran mata ba, idan kun riƙi taƙawa, to kada ku sassabta magana har wanda ke da cuta a cikin zuciyar shi ya yi tsammanin wata sha'awa, kuma ku riƙa faɗin magana ta alheri. Kuma ku kasance a cikin* ***gidajen ku,*** *kuma kada ku yi fita irin yadda (mata) ke fita a zamanin jahiliyar farko.* (Ahzab:32-33)

Abin lura a nan shi ne, Allah (SWT) cewa Ya yi matan Annabi (SAW) su kasance a cikin **gidajen** su ba a cikin **gidan** su ko **ɗakunan** su ba! Wannan ya tabbatar da bayanan masu tarihin Musulunci da suke cewa ko wace matarAnnabi (SAW) tana da gidan ta daban.

Kuma Allah (SWT) Ya ce, a cikin Suratul Ahzab Aya ta 53:-

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَدۡخُلُواْ بُيُوتَ ٱلنَّبِيِّ إِلَّآ أَن يُؤۡذَنَ لَكُمۡ

*Yaku waɗanda suka yi imani, kada ku shiga* ***gidajen*** *Annabi (SAW), sai fa idan ya yi maku iz'ni.*

A nan, Allah (SWT) bai ce **بيت النبى** watau **gidan** Annabi (SAW) ba, sai Ya ce: **بيوت النبى** watau **gidajen** Annabi (SAW).

Waɗannan ayoyi sun nuna cewa matan Annabi Muhammadu (SAW) kowa da gidan ta, watau ba suna a gida guda ba ne ɗakin-wannan yana-kallon-na-waccan. A'a, ko wacce da shiyyar ta ko gidan ta daban. Shafi na 289 na littafin ***Su'aal wal Jawab fil Fiƙhi*** wanda hukumar wallafawa da yin ɗab'i na Dar Al-Manarah da ke El-Mansoura a ƙasar Misra ya wallafa, ya bayyana cewa

matan Annabi (SAW) ko wacce da gidan ta daban; ba wai an haɗa su a gida ɗaya ba ne ko wacce da ɗakin ta.

Kuma a cikin Suratut Talaƙ, Allah (SWT) Ya nuna cewa ba ma matan Annabi (SAW) ba, a'a, har ma na Sahabban shi (RA), gidaje gare su daban domin Allah (SWT) Ya yi umurnin cewa idan aka saki mata to kada a fitar da su daga **gidajen** su (ba **ɗakunan su** ba) Ga abin da Allah (SWT) Ya ce,

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ إِذَا طَلَّقْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَطَلِّقُوهُنَّ لِعِدَّتِهِنَّ وَأَحْصُوا۟ ٱلْعِدَّةَ ۖ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ رَبَّكُمْ ۖ
لَا تُخْرِجُوهُنَّ مِنۢ بُيُوتِهِنَّ وَلَا يَخْرُجْنَ إِلَّآ أَن يَأْتِينَ بِفَٰحِشَةٍ مُّبَيِّنَةٍ ۚ وَتِلْكَ حُدُودُ
ٱللَّهِ ۚ وَمَن يَتَعَدَّ حُدُودَ ٱللَّهِ فَقَدْ ظَلَمَ نَفْسَهُۥ ۚ

*Ya kai Annabi! Idan **kun saki mata, sai ku sake su** a bisa ga Iddar su, kuma ku ƙididdige Iddar. Kuma ku ji tsoron Allah Ubangijin ku. Kada ku fitar da su (matan da aka saki) daga **gidajen su,** su kuma kada su fita sai dai idan sun zo da wata alfashe bayyananniya; dukkan waɗannan dokokin Allah ne kada ku ƙetare su, dukkan wanda ya ƙetare dokokin Allah to, haƙiƙa ya zalunci kanshi.* (Suratut Talaƙ, 65:1)

A nan, ana ƙara nanata cewa idan matan aure su suka yarda a haɗa su gida guda, to shi kenan, sun sarayar da haƙƙin su. Sai dai ko ba-jima ko ba-daɗe, fitinu za su ɓullo kai a cikin irin wannan zama; domin haka ya fi kyau a banbanta masu gida ko kuma ko wacce a fidda mata shiyyar ta daban yadda ba ta ganin ko jin abinda ɗayar ta ke yi ko ta ke ciki.

Za'a fahimci cewa yawancin ƙasashen Musulunci, musamman na Larabawa, tilas ne a raba ma mata gidaje, kusan ma a wasu ƙasashen ba'a ajiye matan aure a unguwa guda balle ma a gida guda! Wannan ya zamo haka musamman sabo da dalillan da suka gabata a sama cikin wannan Babi

## MENE NE HUKUNCIN CIYARWA DA TUFATARWA?

Tsarin ba mata abinci ya faro daga Alƙur'ani da sunnar Ma'aiki (SAW) da Ijma'in malamai. A Al-ƙur'ani mai Girma Allah (SWT) Ya ce:-

لِيُنفِقْ ذُو سَعَةٍ مِّن سَعَتِهِۦ ۖ وَمَن قُدِرَ عَلَيْهِ رِزْقُهُۥ فَلْيُنفِقْ مِمَّآ ءَاتَىٰهُ ٱللَّهُ ۚ لَا يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفْسًا إِلَّا مَآ ءَاتَىٰهَا ۚ

*Mawadaci ya ciyar daga cikin abinda aka wadata shi da shi,wanda kuma aka ƙuntata ma shi arzikin shi, to ya ciyar daga abinda Allah Ya ba shi. Allah ba Ya kallafa ma wani rai face abinda Ya ba shi.* (Suratuɗ Ɗalaƙ-Aya ta: 7)

وَعَلَى ٱلْمَوْلُودِ لَهُۥ رِزْقُهُنَّ وَكِسْوَتُهُنَّ بِٱلْمَعْرُوفِ ۚ لَا تُكَلَّفُ نَفْسٌ إِلَّا وُسْعَهَا

*Haka kuma wajibi ne kan wanda aka yi ma haihuwa, ya azurta su (watau ya ciyar da su) kuma ya tufatar da su da kyakykyawan (tufafi) gwargwadon iko. Ba'a aza ma rai sai gwargwadon abin da ta ke iyawa.* (Suratul Baƙara-Aya ta: 233).

A Hadisin Jabir (RA) Annabi (SAW) Yana cewa:

**اتقوا الله في النساء فإنهن عوان عندكم، أخذتموهن بأمانة الله، واستحللتم فروجهن بكلمة الله، ولهن رزقهن وكسوتهن بالمعروف**

*Kuji tsoron Allah cikin (al'amarin) mata, domin su mataimakan-ku ne, kun auro su cikin amanar Allah, kuma kun halatta farjojin su da kalmar Allah, sabo da haka wajibinku ne ku ciyar da su, ku tufatar da su da kyakykyawan al'amari.* (Sahih-Muslim: 1218).

Mu'awuya Alkushary (RA) ya ce, "na tambayi Ma'aiki (SAW) cewa: menene haƙƙin mace akan ɗayanmu, sai ya amsa da cewa:-

**أن تطعمها اذا طعمت وتكسوها اذا اكتسيت، ولا تضرب الوجه ولا تقبح ولا تهجر الا في البيت**

*Ka ciyar da ita, idan ka ci, ka tufatar da ita, idan ka yi futafi, kada ka bugi huskar ta, kada ka munana mata, idan kun samu saɓani –*

*ka da ka ƙaurace mata, sai fa a cikin ɗaki.* (Sunan Abu Dawud: 2142)

Idan an dubi waɗannan dalillai da kyau, za'a ga cewa wajibi ne ga miji ya ciyar da matar shi, kuma ya tufatar da ita.

## TILAS NE MATAR AURE TA DAFA MA MIJIN TA DA SAURAN MUTANEN GIDA ABINCI?

Maganar dafa ma miji da sauran 'yan gida abinci, wata magana ce wadda malamai suka yi saɓani akai, ra'ayin su ya kasu gida ukku:

**Ra'ayin Farko:-** Malamai masu ra'ayin farko sun ce dafa abinci da yin sauran hidimar mace ga mijin ta ko kuma cikin gida, ba abu ba ne da ya zama wajibi akan ta ba. Domin ita dalilin zuwanta shi ne aji daɗin zama da ita, ba'a sanya ta hidima ta wahala ba, don haka, ba dole ba ne ta yi ma miji girkin abinci, ko sharar gida, ko wanki da sauran su. Wannan shi ne ra'ayin Mazhabar Shafi'iyya, Hambaliyya, Hanafiyya da Malikiyya.Malamai masu wannan ra'ayi sun ce Hadissan da suka nuna cewa mace ta yi ma mijin ta hidima kan kyautatawa ne da ɗa'a (watau ***ihsani*** da ***taɗawu'i)*** amma ba wajibci ba. Waɗannan Malamai suna ganin cewa muddin miji ya na da wadata, to, lallai ya ba matar shi mai yi mata hidimar girki da ayyukan gida.

Mashahurin littafin nan na Mazhabar Malikiyya wanda aka fi sani da suna **"Risala"** wanda Sheik Abu Muhammad Abdullahi ibn Abi Zaid al-Kairawani ya wallafa ya yi bayani akan wannan mas'ala a cikin "Babi kan Idda da Ciyarwa da Tsarki". A shafi na 101 na fassarar wannan littafi wanda kamfanin ɗab'i na Arewa da ke Zariya ya buga a shekarar 1969 an rubuta cewa:-

**وإن اتسع فعليه إخدام زوجته**

*In har miji yana da hali, to, ya samo kuma ya damƙa ma matar sa hadimi (kuku).*

**Ra'ayi na Biyu:-** Malamai masu ra'ayi na biyu sun ce wajibi ne mace ta yi ma mijinta hidima, kuma sun bayyana cewa akwai riwayoyin da ke cewa matan Sahabban Manzon Allah (RA) sun kasance suna yi ma mazajen su hidima da aikace aikacen gida a zamanin Ma'aiki (SAW).

Fatimatuz-Zahrah (RA) ta kai kukanta gidan su, a wajen baban ta Annabi Muhammadu (SAW), don a samar mata da hadimi (wanda zai riƙa tayata aiki), domin hannunta yana yin kanta sabo da niƙa, amma Ma'aiki (SAW) sai ya ce mata, "ku yi tasbihi 33, tahmidi 33, takbiri 33, idan zaku kwanta barci, ya fiye maku wani mai hidima, don taya ku aikace-aikace".

Asma'u bint Sayyidina Abubakar (RA) ta ce, "na kasance ina yi ma miji na Zubair hidimar gida duka, yana da doki, ni ce ke ba shi ruwa da ciyarwa, kuma in share turken shi, in share gida da kuma ɗebo ruwa a tulu da sauransu."

Sheik Ibn Kayyim ya ce:- "Bai inganta ba a banbanta tsakanin mace mai daraja da mace faƙiriya ko marar daraja, ko mawadaciya, a wajen hidimar miji, ga dai matan mafiya daraja nan, matan Sahabbai (RA) suna yi ma mazajensu hidima, har wasu na kai koken wahala, amma ba'a saurare su ba. Sabo da haka, a fili yake cewa Malaman da suka ce mace ta yi ma mijinta hidima, gwargwadon iyawar ta, maganar su tafi inganci, sabo da dalillan da suka gabata. Kuma irin wannan rayuwa ake aiwatarwa a gidajen jama'a (manya da ƙanana) a ko ina a duniyar Musulunci. Amma duk da haka ana taimaka ma mace da mai yi mata hidima gwargwadon ƙarfin miji ko halin shi.A duba cikakken bayani a kan wannan magana ta Sheik Ibn Kayyim a littafin Dr. Muhammad Ibrahim Alhafnawi, mai

suna: *"Almausuu'a Alfiƙhiyya-Almuyassarah-Azzawaj",* Shafi na 295 zuwa na 298.

**Ra'ayi na Ukku:-** Malamai masu ra'ayi na ukku sun tsaya ne tsakanin masu ra'ayi na farko da na biyu suka ce:- abin lura a kan waɗannan ra'ayoyi guda biyu shi ne:-dukkan su sun ta'allaƙa ne da cewa matar aure ta yi ma mijinta hidima ya jingina ne da **kyautatawa** da kuma halin da mijin yake ciki, watau "shi mai wadata ne ko kuma matalauci ne?" Idan mai wadata ne, to tilas ya samo ma matar sa mai yi mata ko ma masu yi mata hidima kamar mai dafa abinci, mai yin shara, mai kula da filawowin gida, mai gadi, mai wanki da guga da dai makamantan su. Idan kuma matalauci ne, to wajibi ne matar ta taimaka masa wajen wasu aikace-aikace.

Watau dai, ko mijin yana da wadata ko baya da ita, to yana daga cikin kyautatawa, matar sa ta yi masa hidima gwargwadon iyawar ta. Misali matar mai wadata, idan kuku ya dafa abinci, to tana iya kaiwa a kan tebur ko shimfida ta ajiye ta kuma kawo ruwa da sauran abubuwan cin abinci. Matar matalauci kuma yana da kyau ta dafa abincin kuma ta kai ma mijin ta. Waɗannan malamai masu ra'ayi na ukku sun nuna cewa Allah (SWT) cewa Ya yi:-" *Wajibi ne suma (mata) su kyautata, kamar yadda aka kyautata masu".* (Suratul Baƙara-Aya ta: 228). Watau dai **kyautatawa** ita ce kalma mafificiya a wannan al-amari. Kuma Sayyidatuna Faɗimatuz-Zahrah (RA) ta kai kukanta gidan su, a wajen babanta Annabi Muhammadu (SAW), don a samar mata da hadimi amma bata roƙi wannan daga mijin ta ba. Da Annabi (SAW) ya so, da sai ya sa a samar mata da mai hidima amma bai yi haka ba domin ya ƙarfafa ma mata su riƙa kyautatawa mazajen su kuma domin kada ya zamo wani abu na tilasci ga kowa da kowa (watau mawadatan dukiya da waɗanda ba su da dukiya).

## HUKUNCIN MIJI YA YI MA MATAR SHI ABUBUWA KAMAR YADDA TA SABA A GIDAN IYAYEN TA

Hukuncin miji ya yi ma matar shi abubuwa kamar yadda ta saba a gidan iyayen ta, ya bi yadda Shari'ah ta shirya domin hukuncin kamar na muhalli ne da ciyarwa da tufatarwa kamar yadda aka yi bayanan da suka gabata akan waɗannan mas'aloli. Ginshiƙin zaman lafiyar aure shi ne mutum ya auro wadda ta dace da shi ba wadda ta fi ƙarfin shi ba. Idan aka auri mace kuma aka kasa bata abubuwan da ta saba da su a gidan iyayen ta, na dangane da muhalli, abinci, sutura da makamantan su, to lallai za'a samu matsala. Amma abin lura a nan shi ne, mutum zai iya auro mace daga gidan mawadata kuma ya zamana shi ma mawadaci ne, amma daga baya wadatar ta kau. A nan ana son haƙuri gwargwadon iko daga ita macen. Su taru su yi ta roƙon Allah Ya fitar da su daga wannan hali.Abin ƙara lura shi ne, lallai miji ya tsare haƙƙoƙin matar sa ita kuma ta tsare na shi. Allah Ya faɗa a wurare da dama a cikin Al-Kur'ani mai tsarki cewa bai aza ma wani mahaluƙi abin da baya iyawa ba. Watau a nan ana iya cewa, a wajen aure, kada mutum ya auro wadda ba ya da **halin** iya riƙawa, domin Allah bai aza masa wannan nauyin ba. Kuma Manzon Allah (SAW) ya jaddada maganar **hali** wajen aure lokacin da ya ke bayani ga wasu matasa, a inda ya ce masu:-

*Ya ku wannan rukunin matasa! Wanda duk ke da **hali** a cikin ku, to, ya yi aure.* (Buhari da Muslim suka ruwaito wannan Hadisi).

Kuma sharuɗɗan da ake ambatawa a lokacin ɗaurin aure sun haɗa da cewa, ciyarwa da tufatarwa da wurin zama da koyar da addini da makamantan su sun tashi daga gidan iyayen matar sun koma a kan mijin ta. Ashe idan namiji baya iya biyan waɗannan buƙatun, to bai halatta ya auri matar ba

# Babi Na Bakwai
# TARBIYYAR ‘YA’YA

An gina al-Ummah (watau community) daga irin gidajen da ke cikin wannan al-Ummah. Kuma irin iyalan da ke cikin waɗannan gidaje su ne ginshiƙai na gina ko na rusa wannan al-Umma. Daɗin daɗawa, yara matasa a ko ina a Duniya su ne suka fi yawa a cikin al-Ummah kuma su ne ruwan sanyaya fitina ko kuma makamashin ruruta fitinar. Don haka ya zama wajibi iyaye su tarbiyantar da ‘ya’yansu su zamo na gari domin ci gaban al-Ummah da Kasashe baki ɗaya. Idan ba’a yi haka ba, to yara matasa za su ruruta fitinu iri-iri waɗanda za su jaza yawan tashin hankula da ruguza al-Ummah.

Musulunci ya Shar’anta ma Musulmi wajibcin tarbiyantar da ‘ya’yan su, domin wannan haƙƙi ne daga cikin haƙƙokin yara akan mahaifan suko walliyan su masu kula da su. Allah Ya ce,

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَأَهۡلِيكُمۡ نَارٗا وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلۡحِجَارَةُ عَلَيۡهَا مَلَـٰٓئِكَةٌ
يُؤۡمَرُونَ مَا وَيَفۡعَلُونَ أَمَرَهُمۡ مَآ ٱللَّهَ يَعۡصُونَ لَّا شِدَادٞ غِلَاظٞ

*Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku ɗauki matakin kare kawunan ku da iyalanku daga wata Wuta wadda makamashinta mutane da duwatsu; masu tsaron ta wasu irin Mala’iku ne masu karfin gaske da tsananin gaske, ba su saɓawa Allah daga abin da Ya umurce su, kuma duk abin da Ya umurce su, shi su ke aikatawa.*(At-Tahrim aya ta 6)

Annabi Muhammadu (SAW) ya ce,

**ألا: كلكم راع، وكلكم مسئول عن رعيته... والرجل راع على أهل بيته، ومسئول عن رعيته، والمرأة راعية على بيت بعلها وولده، وهي مسئول عنهم... (متفق عليه)**

*Kowa ya saurara ya ji: Dukkanku masu kiwo ne, kuma kowanen ku sai an tambaye shi kiwon da aka ba shi… namiji mai kiwo ne game da mutanen gidansa, kuma sai an tambaye shi akan abin da aka ba shi kiwo; mace ma mai kiwo ce a gidan mijinta, da ‘ya’yansa, kuma sai an tambayeta akansu…* (Buhari da Muslim suka ruwaito)

Abdullahi bin Umar (RLA) ya ce ma wani mutum,

*Ka tarbiyantar da ɗanka; don Allah zai tambaye ka a kan sa,watau me ka koya masa; shi kuma Allah zai tambaye shi irin biyayya da kyautatawar da ya yi maka.*

Al-Kur’ani Mai Girma ya kawo ayoyi masu yawa da ke yin magana game da ‘ya’ya. Ga kaɗan daga cikin su:-

1. ‘Ya’ya adon rayuwar Duniya ne, don haka a gode ma Allah da Ya bayar da su (Kahafi: 46)
2. ‘Ya’ya su ne mizanin jarrabawar da Allah ke yi ma iyaye a Duniya, don haka a basu tarbiyya ta gari (Tagabun: 15)
3. Kada iyaye su damu da nauyin da Allah Ya aza masu na ‘ya’yan su, sai su yi hamdala (An'am: 151)
4. Kada iyaye su yi alfahari da yawan ‘ya’yan su (Saba': 35)
5. ‘Ya’yan da ba na kirki ba, ba su da wani amfani ga iyayen su a Lahira (Mumtahannat: 3)
6. Kada ‘ya’ya su hana iyaye tuna Allah (Munafiƙun: 9)
7. Wasu ‘ya’yan (watau na kirki) natsuwar rai ne kuma sanyin idanune ga iyaye, sai a yi hamdala (Furƙan: 74)
8. Wasu daga cikin ‘ya’yan (watau na banza) maƙiya ne ga iyaye, sai a yi hattara (Tagabun: 14)
9. Yi wa ‘ya’ya wa’azi da nasiha wajibi ne (Luƙman: 13)
10. Yi wa ‘ya’ya addu’a ta gari wajibi ne (Ibrahim: 35)

11. Yi wa ‘ya’ya nasiha da wasiyya a ƙarshen rayuwar iyaye kafin mutuwar su wajibi ne (Baƙara: 132)

## KOYAR DA IBADA DA SANA’A DA ZAMANTAKEWA

‘Ya’ya amana ne daga Allah kuma tilas ne Uba da Uwa su kula da renon su ta hanyar kula da fannin rayuwar su da tarbiyyar su har su kai munzalin da Shari’ah ta ƙayyade a basu ‘yancin su. A nan za’a fahinci abubuwa ukku, watau:-

1. A kula da ‘ya’ya tun daga haihuwarsu, zuwa jarintakar su zuwa girman su har maza su balaga, mata kuma su yi aure.
2. A tabbatar da ba ‘ya’ya ilmin ibadar Allah da koyar da yadda ake yin ibadar kamar yadda Musulunci ya zayyana.
3. A tabbatar da ba ‘ya’ya ilmin sana’a da na zamantakewa. Watau a koya masu ilmin zamani ko sana’ar hannu ko kuma duka biyun tare. Kuma a koya masu zamantakewa tsakanin su da sauran jama’a. A nan koyar da gaskiya da riƙon amana da tsare haƙƙin su da na sauran jama’a ya zama wajibi.

Iyaye na da nauyi kwarai a nan kuma Hukuma da sauran al-Ummah su ma suna da nasu nauyin wajen tabbatar da cewa yara sun tashi da ilmi da ɗab’iu kyawawa. Tilas a kula da kawar da duk abinda zai jaza yawon banza da barace-barace tsakanin yara. Wannan shi ne zai kare yara daga shaye-shayen kayan maye da sace-sace da ma ayyukan ta’addanci.

## ILLOLIN RASHIN YI KO SAMAR DA SANA’A

Illolin rashin koyar da sana’a, ko ragganci wajen ƙin yin sana’a, ko rashin samar da hanyoyi na yin sana’a, suna kawo zaman banza wanda ke haifar da illar bara, roƙo da maula. Waɗannan illoli sun yi katutu a kan yara Musulmi da ke bin tituna da gidaje da sauran wuraren zaman mutane suna bara, roƙo ko maula har

abin ya kai fagen ana ganin kamar Musulunci ne ya zayyana yin hakan. Amma a fili yake cewa Manzon Allah (SAW) da Sahabban sa (RLA) da duk mutanen ƙwarai da suka shuɗe sun nuna yadda Musulunci bai yarda da ragganci ba. Allah Shi ne mai kowa mai komi, kuma Ya bayyana cewa mutane su tashi tsaye a kan dukkan al-amurra, sannan Shi taimaka masu.

Domin sanin irin muhimmancin yin sana'a sai a dubi Hadisin da Abu Abdullah Zubair bin Awamm (RLA) ya faɗa cewa Manzon Allah (SAW) ya ce,

**لأَنْ يَأْخُذَ أَحَدُكُمْ حَبْلَهُ فَيَأْتِيَ بِحُزْمَةِ الْحَطَبِ عَلَى ظَهْرِهِ فَيَبِيعَهَا فَيَكُفَّ اللَّهُ بِهَا وَجْهَهُ ، خَيْرٌ لَهُ مِنْ أَنْ يَسْأَلَ النَّاسَ أَعْطَوْهُ أَوْ مَنَعُوهُ.**

*Wanin ku ya ɗauki igiya ya tafi daji, ya wo itace, ya ɗauko, ya sayar domin Allah ya tsare masa mutuncinsa, ya fi alkhairi agareshi da ya tafi yana roƙon mutane su taimaka masa, sun bashi ko basu bashi ba.* (Bukhari da Muslim suka ruwaito).

Bukhari da Muslim sun ruwaito a cikin Sahihansu cewa Abu Huraira (RLA) ya kawo Hadissai guda ukku in da ya ke cewa,

(1) Manzon Allah (SAW) ya ce, *"Annabawan Allah suna da sana'ar kiwon dabbobi".* Sai aka tambaye shi cewa har da kai ya Manzon Allah? Sai ya ce, *"Ba shakka na yi kiwo kuma ana biya na wasu 'yan kuɗi kaɗan".*

(2) Annabi (SAW) ya kuma ce,

**أَنَّ دَاوُدَ ـعَلَيْهِ السَّلاَمُ ـ كَانَ لاَ يَأْكُلُ إِلاَّ مِنْ عَمَلِ يَدِهِ**

*"Annabi Da'ud (AS) ya kasance baya ci sai daga abinda hannun sa ya aikata"*, (watau daga sana'ar ƙira)

(3) Kuma Annabi (SAW) ya ce, *"Annabi Zakariya kafinta ne".*

Kuma a shafi na 237 na cikin littafin "*Islam wal Idara*" an bayyana cewa Al-Hakim ya ruwaito Annabi (SAW) yana cewa,

*Annabi Adamu manomi ne, Annabi Nuhu kafinta ne, Annabi Idris tela ne, Annabi Musa makiyayi ne".*

Sahabbai da Tabi'ai da Tabiut-Tabi'ina duk suna kasuwanci, noma, kiwo ko wata sana'a. Duk mutanen kirki a cikin Musulunci kamar su Shehu Usman Danfodiyo, suna da hanyar neman abinci. Shehu Danfodiyo da mabiyansa duk makiyaya ne ko manoma ko masu fatauci. Idan Annabi Muhammadu (SAW) da sauran Annabawan Allah (AS) da Sahabban su (RLA) da sauran mutanen kirki a cikin Musulunci duk suna da sana'ar yi, to, wace hujja wani mutum yake da ita da ya ke zaune yana jiran wasu mutane su bashi abin masarufi? Kuma wace hujja wani mutum ya ke da ita da ya ke tura 'ya'yan sa ƙanana su tafi suna bara? Rayuwar Annabi (SAW) da Sahabban sa (RA) da sauran mutanen kirki a cikin addinin Musulunci tilas su zamo abin koyi, muddin dai ana son samun lafiya da zama lafiya da abinda lafiya zata ci.

Don haka wajibi ne iyaye, da Hukuma da suaran al-Ummah su tashi tsaye su koyar da sana'oi kuma a samar da hanoyoyin yin sana'oin domin a kauda barace-barace, musamman ga matasa da sauran masu ƙarfin iya yin sana'a.

**Matashiya**:- Anan ya kamata a tuna ma Shugabanni cewa, Hukuma ke da nauyi wajen tabbatar da cewa an yi amfani da tattalin arzikin ƙasa kowa ya amfana. Aikin Hukuma ne ta tabbatar da cewa an ɗauki duk matakin da ya kamata domin jama'a su samu lafiya, da zama lafiya, da samun ilmin addini, da horo a kan sana'oi. Sannan lallai Hukuma ta taimaka ma mutane su samu abin yi, musamman ta hanyar taimaka masu wajen samun walwalar kafa nasu wuraren sana'ar, yin noma ko yin kiyon dabbobi. Attajirai kuma tilas su riƙa fidda Zakka kuma suriƙa taimaka ma gajiyayyu da miskinai.

# Babi Na Takwas
# MAS'ALOLIN SAKIN AURE

Hadisi na 2178 a cikin Sunan Abu Dawud ya ruwaito Manzon Allah (SAW) yana cewa, ***"Sakin aure shi ne abu halal wanda Allah Ya fi ƙi".*** Sheikh Aliyu Muhammad Salisu ya yi bayanai masu kyau a shafin intanet na "www.munbarin-musulunci.blogspot.com"a kan sakin aure. Shehun Malamin ya ce, Musulunci bai shar'anta yin saki don cutar da wani ɓangare ba, hasali ma Musulunci ya shar'antar da haka ne domin ceto ma'aurata daga mawuyacin hali. Yana daga cikin rahamar Musulunci tabbatar da yin saki, domin Musulunci bai yarda a cutar da kowa ba. A lura, idan aka ce a zauna babu maganar cewar akwai rabuwa ga duk wanda ya ga ana zaluntar shi, kuma ya yi iyakar haƙuri da zai iya yi, to wannan zai ba abokin zaman shi tunanin cewa yana da gata a Musulunci ta ya yi yadda ya ga dama. Lokutta da yawa akan sami miji yana ɗanɗana wa matar shi azaba, ko matar tana zabga wa mijin ta ta'asa, to shin a nan za'a sa ido ne a yi ta kallon su a cikin wannan yanayi? A'a, tilas ne a san irin matakin da za'a ɗauka, daga cikin irin matakan da Musulunci ya shinfiɗa.

Idan saɓani ya shiga tsakanin miji da mata, Musulunci ya yi umurnin a yi ƙoƙarin sasanta su don a hana rabuwar aure. Da farko ya kamata miji, domin shi ke babba, ya yi duk irin ƙoƙarin da zai iya domin yin haƙuri da matar shi kuma ya yi ta yi mata nasiha da fatan za ta gane, har Allah Ya sa su daidaita. Idan ma mijin ke da laifi, to, ya kamata matar ta yi haƙuri kuma ta yi ma mijin ta nasiha ko da Allah zai sa ya gane. Idan wannan ya gagara, sai abokai su yi ƙoƙarin shiga tsakani. Idan wannan ma ya gagara sai a bi mataki na gaba inda Allah (SWT) Ya umurci dangin miji da na mata da su tura wakillai daga kowane ɓangare

na mijin da matar domin a sasanta su. Waɗannan wakillai za su nazarci al’amarin kuma su saurari dukkan ɓangarorin biyu su kuma yi ƙoƙarin daidaita tsakanin su. Allah (SWT) Ya ce,

وَإِنْ خِفْتُمْ شِقَاقَ بَيْنِهِمَا فَٱبْعَثُوا۟ حَكَمًا مِّنْ أَهْلِهِۦ وَحَكَمًا مِّنْ أَهْلِهَآ إِن يُرِيدَآ إِصْلَٰحًا

يُوَفِّقِ ٱللَّهُ بَيْنَهُمَآ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا خَبِيرًا

*Idan kuka ji tsoron saɓanin su (miji da mata) to ku tura wani mai hukunci daga dangin shi (mijin) da kuma mai hukunci daga dangin ta (matar), muddin sukai nufin gyara, to, Allah zai daidaita tsakanin su. Ba shakka Allah masani ne (da abin da ke sarari kuma) masani ne (da abinda ke ɓoye).* (Suratun Nisa’i, 4:35)

فَلَا جُنَاحَ عَلَيْهِمَآ أَن يُصْلِحَا بَيْنَهُمَا صُلْحًا ۚ وَٱلصُّلْحُ خَيْرٌ ۗ

*Babu laifi garesu (miji da mata) idan suka daidaita yin ingantaccen sulhu tsakanin su; domin yin sulhu shi ne mafi alheri* (Nisa’i, 4:128)

Waɗannan ayoyi sun nuna cewa Allah (SWT) ba Ya son rabuwar aure, domin haka ya zama wajibi mutum ya yi haƙuri kuma idan ta kama, ya daure ya sassafta wasu haƙƙoƙin shi domin ganin an sami daidaituwa; domin daidaituwa ta fi rabuwa muddin ba akan saɓawa Allah da Ma’aikinShi bane. Lokaci da yawa mata su kan yi haƙuri da wani haƙƙin su kamar yadda maza suma su kan yi haƙuri da nasu haƙƙin domin ganin aure ya tabbata. Masu iya magana su na cewa, “tsakanin harshe da haƙori ma ana saɓawa – sai ka ga haƙori ya cije harshe!” Kuma, “wanda ya ce maka zo mu zauna, to, ya ce maka zo mu saɓa”.

A lura cewa, ba shakka da za’a riƙa bin matakan da aka ambata na yin sulhu, tun daga sasantawa da juna, zuwa shiga tsakani da abokai za su yi har zuwa lokacin da mahukunta daga iyalan biyu

(watau dattawa daga ɓangaren miji da ɓangaren mata) za su zo domin daidaita tsakanin ma’auratan, to, ba shakka da zai zama da wuya a riƙa sakin aure. Kuma idan har waɗannan matakan ba su biya buƙata ba, to zama tsakanin mijin da matar ba wuya kaɗai zai yi ba, har ma zai iya zama cutarwar da za ta iya haddasa masifar da za ta ayyana yin da-na-sani. A nan rabuwar aure ne mafita, domin al’amarin ya zama muƙaddari daga Allah.

**Adadin Sakin Aure.**

Idan Allah Ya ƙaddara sai an rabu, to, ba makawa sai haka ya faru, kuma addinin Musulunci ya tsara yadda sakin zai kasance, Allah Ya ce,

ٱلطَّلَٰقُ مَرَّتَانِۖ فَإِمۡسَاكُۢ بِمَعۡرُوفٍ أَوۡ تَسۡرِيحُۢ بِإِحۡسَٰنٖۗ

*Saki dai (wanda zai yiwu ai kome akan shi) karo biyu ne, (Miji na da zaɓin) riƙe (matar) yadda ya kamata ko su rabu cikin kyautatawa* (Suratul Baƙara, 2:229).

A nan an nuna cewa miji zai iya sakin matar shi kuma ya iya komar da ita har sau biyu muddin dai ba ta gama Idda ba. Wannan wata hikima ce mai nuna ma miji cewa abin da Musulunci ya fi so shi ne ayi saki ɗaya ba biyu ba gaba ɗaya, domin a samu damar fahimtar wanda ke da laifi tsakanin miji da mata domin a gyara. Bayan an daidaita kuma miji ya mayar da matar shi, amma hali ya sanya dole a ƙara yin saki, to, sai a ƙara yin na biyu. Amma daga nan sai miji da mata su shiga taitayin su na kulawa da haƙƙoƙin da Musulunci ya ɗora akan kowannen su domin ana ƙara yin saki na ukku, to, ba damar yin kome sai an cika wasu sharuɗɗa. Watau, sai ta gama Idda, sannan sai ta auri wani mijin kuma sun yi kwanan aure sannan sun rabu da wannan mijin ba tare da sun yi shirin rabuwa ta hanyar yaudara ba. Daga nan mijin farko na iya

neman sabon auren matar, amma bayan ta gama Iddar sabon mijin da ta rabu da shi. Allah (SWT) Ya ce,

فَإِن طَلَّقَهَا فَلَا تَحِلُّ لَهُۥ مِنۢ بَعۡدُ حَتَّىٰ تَنكِحَ زَوۡجًا غَيۡرَهُۥۗ فَإِن طَلَّقَهَا فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡهِمَآ
أَن يَتَرَاجَعَآ إِن ظَنَّآ أَن يُقِيمَا حُدُودَ ٱللَّهِۗ وَتِلۡكَ حُدُودُ ٱللَّهِ يُبَيِّنُهَا لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ

*To idan ya sake ta (saki na ukku) bata halatta a gare shi sai ta auri wani mijin da ban. Idan sabon mijin ya sake ta, babu laifi su maida aurensu (da mijin farko) in sun san za su bi dokokin Allah. Waɗannan dokokin Allah ne da Ya ke bayyana su ga al-ummah masu tunani* (Baƙara,2:230)

Manzon Allah (SAW) cewa ya yi, a cikin wannan hali sai sabon mijin ya yi kwanan aure da matar kuma sun rabu sannan tsohon mijin ya ke da damar neman ta da sabon aure. A lura a nan cewa an ba miji damar ya bi a hankali wajen yin saki amma sai ya yi gaggawa; domin wauta ma sai ka ga wani mijin duka saki biyun yake yi lokaci guda wani kuma da ya fi wannan wauta sai ya yi saki ukkun ma gaba ɗaya! Irin waɗannan mazaje ne ke dawowa suna neman wai malamai su yi masu fatawar yiwuwar maido da matar bayan saki ukku, ba tare da ta yi wani auren da aka yi kwanan aure da ita ba! To, wannan bai yiwu wa, haramun ne.

**Yin Idda**

Wani babban al'amari shi ne yadda ake gudanar da idda ta haramtacciyar hanya wadda Shari'ah bata yarda da ita ba kuma wadda Allah (SWT) da Manzon Shi (SAW) suka haramta. Idan miji ya saki matar shi sai ka ga ya sallame ta domin ta tafi gidan su, ko kuma ita ta sallami kan ta zuwa gidannsu, domin yin Idda. Wani lokacin ma sai ka ga miji ya watsar da kayan matar a waje ko ya ɗauko mota domin a kwashe mata kayanta; ko kuma ita ta ce ai tana da gidan ubanta bari ta tafi da dai sauran irin waɗannan

munanan ɗabi'u da kalamai waɗan da Musulunci bai amince da su ba. Yin haka haramun ne, Allah Ya ce,

وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ رَبَّكُمْ ۖ لَا تُخْرِجُوهُنَّ مِنۢ بُيُوتِهِنَّ وَلَا يَخْرُجْنَ إِلَّآ أَن يَأْتِينَ بِفَٰحِشَةٍ
مُّبَيِّنَةٍ ۚ وَتِلْكَ حُدُودُ ٱللَّهِ ۚ وَمَن يَتَعَدَّ حُدُودَ ٱللَّهِ فَقَدْ ظَلَمَ نَفْسَهُۥ ۚ

*Kuma ku ji tsoron Allah Ubangijin ku. Kada ku fitar da su (matan da aka saki) daga gidajen su, su kuma kada su fita sai dai idan sun zo da wata alfasha bayyananniya; dukkan waɗannan dokokin Allah ne, kada ku ƙetare su; duk wanda ya ƙetare dokokin Allah to, haƙiƙa ya zalunci kan shi.* (Suratuɗ Ɗalaƙ, 65:1)

**Hikimar Yin Idda a Gidan Aure**

Lallai duk abin da Allah (SWT) Ya tsara ma Ɗan Adam, to, akwai hikimomi da alherai masu yawa a ciki, ko mutane sun sani ko ba su sani ba. Kuma ba'a ɗora ma Ɗan Adam cewa dole sai ya san hikimar abin kafin ya aiwatar da shi, a'a, idan Allah Ya yi umurni, tilas ne a bi wannan umurnin. Ba shakka duk mijin da ya rabu da matar shi ta hanyar saki ɗaya ko biyu, to, tana nan a matsayin matar shi har tsawon lokacin iddar ta, domin wani ba zai zo zawarci ba, idan kuma mijin ya rasu a cikin lokacin iddar, matar za ta gaje shi, kuma za ta yi mashi takaba.

Kuma tun da matar tana Idda a gidan mijin, zai iya mayar da ita a duk lokacin da ya ke so ba tare da an sake ɗaura aure ba domin bata kammala Idda ba; kuma ba sai ya aika masu yin biko zuwa gidan mahaifan ta ba, balle a yi ta kace-nace.

**Sauran Mas'aloli da Suka Jiɓinci Sakin Aure**

Musulunci ya hana sakin mace lokacin da take cikin al'ada, domin Sayyidina Umar (RA) ya tambayi Manzon Allah (SAW) cewa ɗanshi Abdullahi (RA) ya saki matar shi tana cikin al'ada.

Sai Manzon Allah (SAW) ya umurci Sayyidina Umar (RA) da ya umurci ɗan na shi Abdullahi (RA) ya dawo da matar, ta zauna ƙarƙashin shi har sai ta kammala wannan al'adar kuma ta sake yin wata ta kamala sannan in ya ga yiwuwar ya saketa sai ya saketa, kuma aka lissafa wannan sakin cikin sakin na shi. (Bukhari da Muslim suka ruwaito wannan Hadisin).

Idan miji ya saki matar shi, to, ba za'a raba kwana da girki da ita ba, amma tilas ne a ci gaba da bata abinci da sauran kulawa har ta gama Idda. Kuma zata riƙa yin kwalliya da sauran abubuwan jawo sha'awar mijin; ko da zai canza ra'ayi ya mayar da ita, tunda dama tana cikin gidan shi ne lokacin yin Iddar. Wannan wata hikima ce da Musulunci ya tsara domin dai kada mata da miji su rabu. Domin ƙarin bayani a kan kula da matar da ke Idda sai a duba Allah (SWT) yana cewa cikin Suratul-Baƙara aya ta 241, da Suratul-Ahzab aya ta 28 da ta 49. Waɗan nan ayoyi suna daga cikin ɗinbin ayoyin Al-Kur'ani mai Girma da suke ceto mata daga cikin baƙin ƙangin da suka sami kansu a tsarin da ba na Musulunci ba, inda ake mayar da mata kamar rigunan sanyawa – watau a sanya wannan yanzu, kuma idan an ga dama a cire a sanya waccan!Kamar yadda a lokacin ɗaurin aure sai da aka kafa shaidu, to, haka nan lokacin rabuwar aure ma sai an kafa shaidu. Musulunci ya yi umurnin kafa shaidu na aƙalla Dattijai/Adilai biyu ko kuma miji ya bayar da takardar saki mai ɗauke da sanya hannun shi da kuma kwanan wata. Idan mijin bai iya rubutu ba, sai wanda ya rubuta mashi takardar ya rubuta sunan shi da adireshin shi da hannun shi; kuma a dangwala ɗan yatsan mijin a kan takardar. Game da tsaida shaidu a wajen sakin aure, Allah (SWT) Ya ce,

فَإِذَا بَلَغۡنَ أَجَلَهُنَّ فَأَمۡسِكُوهُنَّ بِمَعۡرُوفٍ أَوۡ فَارِقُوهُنَّ بِمَعۡرُوفٖ وَأَشۡهِدُواْ ذَوَيۡ عَدۡلٖ
مِّنكُمۡ وَأَقِيمُواْ ٱلشَّهَٰدَةَ لِلَّهِۚ

*Idan su ka cika Iddar su, ko dai ku riƙe su bisa kyautatawa ko ku rabu da su bisa kyautatawa. Kuma ku shaidawa Adilai biyu daga cikin ku, a kuma tsayar da shaidar domin Allah.* ( Ɗalaƙ, 65:2).

Kome (watau mayar da matar da aka saki) yana kasancewa ne lokacin da miji ya rabu da matar shi ta sanadiyyar saki ɗaya ko biyu, a nan miji na iya mayar da matar shi muddin dai ba ta gama Idda ba kuma muddin sun yi nufin gyara (watau miji da mata). Allah (SWT) Ya na cewa,

وَبُعُولَتُهُنَّ أَحَقُّ بِرَدِّهِنَّ فِي ذَٰلِكَ إِنۡ أَرَادُوٓاْ إِصۡلَٰحٗاۚ

*Kuma mazajen su sune mafi cancantar su mayar da su (matansu) matuƙar sunyi nufin gyara.* (Suratul-Baƙara, 2:228)

Wannan ya nuna cewa duk lokacin da miji ya mayar da matar shi kafin ta gama Iddar saki ɗaya ko biyu da ya yi mata, muddin akwai nufin yin gyara, to, babu wata-wata sai ta koma gare shi.

Amma idan ya kasance saki Ukku ne, to, a nan ba damar yin kome sai an cika wasu sharuɗɗa. Watau, sai ta gama Idda, sannan sai ta auri wani mijin kuma sun yi kwanan aure sannan sun rabu da wannan mijin ba tare da sun yi rabuwa ta hanyar yaudara ba. Daga nan mijin farko na iya neman sabon auren matar, amma bayan ta gama Iddar sabon mijin da ta rabu da shi.

# Babi Na Tara
# RENON YARA DA KULA DA DUKIYAR SU

Rabuwar aure ta kan jaza jayayya a kan renon yara da kula da dukiyoyin su, musamman idan ɗaya daga cikin ma'auratan ya mutu. Tilas ne a yi la'akkari da cewa renon yara shi ma yana da sharuɗɗa da yawa waɗanda tilas ne a bi su. Amma a halin yanzu, ana fama da jayayya a kan wannan mas'ala kuma yawanci ma akan yanke hukuncin da ba shi Musulunci ya shimfiɗa ba.

A wannan Babi an duba mas'aloli guda biyu waɗanda kusan su ne suka fi damun Musulmi game da maganar rabuwar aure a wannan zamani, watau mas'alar **renon yara** da kuma sha'anin **kula da dukiyar su** har su kai munzalin zaman kawunan su da kula da dukiyoyin su. Kuma Babin ya kawo hukunce-hukunce daga wasu Maz'habobi a kan wannan mas'ala domin faɗaɗa ilmi, amma ya fi bada muhimmanci akan Maz'habar Imam Malik domin ita aka fi yin amfani da ita a ƙasashen Afirka Ta Yamma.

## Mene Ne Renon Yara A Musulunci?

A Musulunci an kasa reno kashi biyu, watau renon yara da renon dukiyoyin su (kula da dukiyoyin su). Ga bayanai a taƙaice game da waɗannan hanyoyin reno guda biyu kamar haka:-

1. **Renon yara** yana nufin kula da su tun daga shayar da su nono, yi masu wanka da wanki da koya masu halayen rayuwa na gari tun suna ƙanana. Musulunci ya jingina wannan aiki ne ga mata domin su suka fi dacewa sabo da irin halitta da tausayi da Allah (SWT) Ya ba su. Watau a nan taushin zuciya da haƙuri a ke buƙata wadda ya yi dai-dai da abinda mata za su iya bayar wa. Kuma ba sai an faɗa ba, mata kaɗai ke iya shayar da nono domin Allah bai halicci maza da nono ba!

2. **Renon dukiyar yara** yana nufin kula da dukiyar su har su girma su yi hankali da basirar da za su iya kula da ita da kawunan su. Musulunci ya jingina wannan aiki ga maza domin su suka fi dacewa sabo da su ke iya zirga-zirga domin juya dukiyar da sarrafa ta, ta hanyar da za ta ƙaru. Watau a nan ƙarfi da zarafin shige-da-fice ake buƙata wanda Allah (SWT) Ya ba maza.

**Renon Yara Domin Kula Da Su**

Filin Webisayit (Website) na Cibiyar Musulunci ta***Darul Iftaa*** mai adireshi kamar haka:- www.daruliftaa.com an yi bayanai masu inganci a kan renon yara. Wannan Cibiya an kafa ta ne domin yin fatawa a kan al'amurran addinin Musulunci. Wasu Malamai Musulmi ne suka kafa ta a ƙarƙashin jagorancin Mufti Abu Abdullah Muhammad ibn Adam al-Kawthari wanda Allah Ya yi ma baiwar hardace al-Kur'ani Mai Tsarki tun yana ɗan shekaru tara a duniya. Kuma ya samu ijaza a kan littattafai da dama na addinin Musulunci har da na mashahuran masu Hadissan nan guda shidda (watau *Sittu Sihah*). Shehun Malami Muhammad ibn Adam ya yi karatu a ƙasashe da dama na duniya kuma yanzu yana koyar da Tafsir da Hadith da Fiƙh a *Jami'ah Uloom al-Kuran,* watau Jami'ar Koyon Ilmi al-Kur'ani.

Shehun Malami Muhammad ibn Adamya bayar da fatawa mai inganci a kan renon yara a cikin addinin Musulunci. Ya fara da Hadisi na 2178 a cikin *Sunan Abu Dawud* inda aka ruwaito Manzon Allah (SAW) yana cewa, *"Sakin aure shi ne abu halal wanda Allah Ya fi ƙi"*.

Watau Allah (SWT) ba Ya son a saki aure ko misƙala zarratin. Malamin ya ci gaba da cewa **yara dai amana ne daga Allah** kuma tilas ne Uba da Uwa su kula da renon su ta hanyar kula da fannin tarbiyya har su kai munzalin da Shari'ah ta ƙayyade a basu

‘yancin su. Idan tilasci ya sa aka saki aure ko kuma ɗaya daga cikin ma’auratan ya mutu, to sai a bayar da reno ta hanyar da Shari’ah ta shinfiɗa.

Shehun Malami Muhammad ibn Adam ya ci gaba da cewa, Uwa ita ke da haƙƙin renon yaro har ya kai munzalin yana iya kula da kan sa, kamar cin abinci, wanka da wanki da sanya tufafi. Imam al-Haskafi ya ce, *“renon yaro yana hannun uwa har yaron ya iya kula da kan sa. An ƙiyasta cewa wannan yana iya faruwa idan yaron ya kai shekaru bakwai a duniya kuma an yi fatawa akan wannan shekaru domin yara maza na iya kula da kawunan su a waɗannan shekaru”.* Wannan bayani yana cikin shafi na 566 na Vol. 3 na littafin *Radd al-Muhtar* na Sheik ibn Abidin. Shafi na 237 na littafin *al-Mawsili, al-Ikhtiyar li ta’lil al-mukhtar* Kashi na 3, ya bayyana cewa Uwa ke da renon yarinya har yarinyar ta balaga ko kuma ta kai kimanin shekaru tara a duniya. Wannan dama da aka ba Uwa na renon yara tana kuɓucewa idan Uwar:-

1. Ta fita daga addinin Musulunci
2. Tana alfasha wadda zata iya cutar da yaran
3. Bata kula da yaran sabo da tana barin gida akai-akai
4. Ta auri wanda ba dan-uwan jini bane ga yaran
5. Ta nemi a biya ta domin kula da yaran alhali akwai wadda zata kula da su kyauta

Ana ƙara ƙarfafa cewa renon yaro yana farawa daga Uwa daliln Hadisin da aka ruwaito cewa wata mata ta je wajen Manzon Allah (SAW) tana kukan cewa mijinta ya sake ta kuma yana son ya amshe mata yarinya, sai Annabi (SAW) ya ce mata, *“Ke ce kika fi dacewa da riƙon yarinyar muddin dai baki yi wani aure ba”.* (*Sunan Abu Dawud,* Hadisi mai lamba 2276 da kuma *Mustadrak al-Hakim*Vol.2 shafi na 207).

A shafi na 261 zuwa shafi na 266 na Littafin TUHFATUL HUKKAM wanda marigayi Alƙalin Alƙalan Jihar Katsina, Alhaji Usman Muhammad Daura ya fassara da sunan JAGORAR MASU HUKUNCI, kuma wanda aka fi amfani da shi a Maz'habar Malikiyya, an yi bayanai masu tsawo da inganci a kan renon yara.

Shafi na 262 ya yi bayanin sifar masu reno kamar haka:- *"Sanya reno a hannun mata shi ne ya fi dacewa, maimakon sanya shi a hannun maza, saboda abin da ake nufi da reno shi ne, kula da yaro, don shi yaro halitta ce mai rauni, ba zai iya sarrafa al-amurran sa ba, sabo da haka Shari'ah ta sanya renon sa a hannun wanda ya fi tausayi a kan yaron, ga al'ada su ne mata. Kuma sharaɗi ne mai reno ta zamo tana daga cikin ma'abutan zumuncin wanda za'a rena, kuma ta zamo daga cikin ma'abuta haramcin sa, watau waɗanda babu aure tsakanin sa da su, ko da ya girma".*

Shafi na 263 ya yi bayanin tsawon lokacin da za'a riƙe yaro a reno kamar haka:- *"Iyakar lokacin da za'a riƙe yaro a reno idan namiji ne, shi ne har zuwa sa'ar da ya balaga, bisa ga zance wanda ya ke mashahuri… amma mace renon ta yana ƙarewa sa'ar da ta yi aure kuma mijin ta ya yi dukhuli da ita".*

Kuma a shafi na 262 zuwa na 265 an yi bayanai a kan jerin masu yin reno a matakan darajar su, watau macen da zata fara reno da mai bi mata da mai bi ma wannan har zuwa lokacin da reno zai koma ga maza. Ana iya taƙaita wannan jeri na masu reno kamar haka:-

1. Uwa ita ta fi kamata ta reni ɗanta,
2. sannan Uwarta, watau Kakar wanda za'a rena,
3. sannan *Khalah* watau Yayar Uwar wanda za'a rena,
4. sannan Kanwar Uwar wanda za'a rena,
5. sannan Uwar Uba watau Kakar wanda za'a rena,

6. sannan Uban wanda za'a rena,
7. sannan Yayar Uban wanda za'a rena,
8. sannan Ƙanwar Uban wanda za'a rena,
9. sannan Yar-Uwan wanda za'a rena,
10. sannan Ɗiyar Ɗan-Uwan wanda za'a rena,
11. sannan Ɗiyar Yar-Uwan wanda za'a rena,
12. sannan Ɗan-Uwan wanda za'a rena,
13. sannan wanda Uba ya baiwa wasiyya
14. sannan Asibai.

Hukumar Musulunci ce zata tabbatar da cewa an bi tsarin da Musulunci ya shimfiɗa wajen reno, kuma Hukumar na iya amshe renon yaran idan suna cutuwa, domin ta damƙa su ga inda ba zasu cutu ba, amma bisa sharuɗɗan da Shari'ah ta shimfiɗa.

Shafi na 264 ya yi bayanin cewa idan reno ya kuɓuce wa Uwa kuma ita ce ta jawo dalilin da renon ya kuɓuce mata, misali idan ta watsar da yaron ta yi tafiyar ta, to, ko dalilin ya gushe, renon ba zai dawo gare ta ba. Malamai sun ce haka ma wannan hukuncin ya ke a kan maza. Kuma idan wanda ke da haƙƙin renon yaro ya ƙi neman haƙƙin sa har tsawon shekara guda, to, shi ma ya sarayar da haƙƙin sa. Hakanan idan mai haƙƙin reno da kan sa ya ce ya saki haƙƙin, to, wannan haƙƙin ba zai sake komawa a gare shi ba.

**Matashiya-** Ya kamata a lura da cewa ko ma wanene renon ke hannun sa (watau Uwa ko Uba), ɗayan yana da damar ya riƙa ganin yaran akai-akai. Kuma ko da yaushe wani daga cikin iyayen ya ziyarci yaran tilas ne a nuna masa su. Sannan, a ko yaushe, Uba ke da haƙƙin bayar da wurin kwanan yaran idan Uwar bata da shi; da haƙƙin ciyarwa da suturtawa da dai biyan sauran buƙatun yaran gwargwadon ikon sa. Wannan haƙƙin yara yana nan kan Uba, idan 'yan-mata ne, to har su yi aure idan 'yan-maza ne kuma har su balaga. Idan kuma yaron ko yarinyar musakai ne

to haƙƙin Uba ne ya kula da su tsawon rayuwar su. (a duba littafin *Radd al-Muhtar* na Ibn Abidin domin ƙarin bayani).

**An yi bayanin dalillan ba mata reno** a cikin littafin, *Wilaayat al-Mar'ah fi'l-Fiƙh al-Islami*, shafi na 692, kamar haka:- Musulunci ya jingina wannan aiki na renon yara ga mata domin su suka fi dacewa sabo da irin halitta da tausayi da Allah (SWT) Ya ba su. Watau a nan taushin zuciya da haƙuri a ke buƙata wanda ya yi dai-dai da abinda mata za su iya bayar wa. Uwa da sauran mata suna da wannan dama ta reno muddin dai sun cika ƙa'idojin da Shari'ah ta shinfiɗa waɗanda suka haɗa da:-

1. Musulma ba kafira ba
2. Baliga, mai hankali da kula
3. Ɗiya ba baiwa ba
4. Mai halin kirki ba ashararriya ba
5. Kada ta auri wanda bai da dangantaka ta jini da yaron
6. Ta zama mazauniyar garin da Uban yaron yake

Abin ƙara kula a kai a nan, shi ne, lallai a yi la'akkari da cewa duk abinda za'a yi, to ya zama burinsa shi ne rayuwar yaran ta zamo ingantatta kuma mai kyau ba wai a biya ma Uba ko Uwa buƙata ba. A nan ne Hukumar Musulunci ta shigo. Domin ita ce ke da ƙarfin tabbatar da cewa an bi tsarin Shari'ah a wajen reno.

**Fatawar Zamani A Kan Renon Yara**

Bayar da renon yara ga Uwa yana da wata sarƙaƙƙiya wadda ke ruɗa mutane musamman a cikin Maz'habar Imam Malik, inda aka ce "***Uwa ke da renon yaro har ya balaga, yarinya kuma har ta yi aure kuma mijin ya yi jima'i da ita***". A nan, yawanci a kan fahimci cewa ko Uwar tana auren Uban yaran ko bata auren sa, wannan haƙƙi nata yana nan daram. To, ba haka al-amarin yake ba. Wannan haƙƙi na Uwa tayi renon yara har wannan tsawon

lokaci ya danganta da idan tana auren Uban yaran ne. Idan bata auren sa, to sai a koma ma matakan renon da aka riga aka yi bayanin su a cikin wannan littafi.

Shehun Malami Abu Bakr Jabir Al-Jaza'iry na ɗaya daga cikin manyan malaman da Allah ya basu falalar zama masu wa'azi na din-din-din (watau "permanent lecturer") a Massalacin Annabi (SAW) da ke Madina, ya yi bayani a kan mas'alar RENON YARA a shafi na 394 da na 395 a cikin liffatin sa mai suna, *Minhaj Al-Muslim*Vol. 2, wanda kamfanin ɗab'i na DARUSSALAM da ke birnin Riyadh na ƙasar Saudiya ya ɗabba'a a shekarar 2001 Miladiya. Shehun Malamin ya wallafa littafin acikin harshen Larabci. Kwamitin Masu Fassara na kamfanin ɗab'i na Darussalam sun fassara littafin zuwa harshen Turanci a ƙarƙashin jagorancin Dr Abdul Malik Mujahid.

Bayanin Shehun Malamin ya zo a taƙaice, kamar haka:- Muddin aure ya rabu, to Uwa na da ikon reno ne har yara (maza da mata) su kai shekaru bakwai (7) a duniya daga nan sai Uba ya amsa! Faƙat!Ga abin da Shehun Malamin ya ce:-

*"Lokacin da Uwa zata reni yaro zai zamo har ya zuwa balagar sa, yarinya kuma har ta yi aure kuma mijin ta ya yi jima'i da ita. Amma idan an raba auren Uwar da Uban yaran, to Uwar zata reni yarinya har ta kai shekaru bakwai (7) a duniya, daga nan sai a maida ta wajen Uban ta domin shi ya fi dacewa da kula da tsaro da zayyana hankali da tarbiyyar yarinyar amma ba mata ba. Idan kuma yaro ne wanda ya kai shekaru bakwai (7) a duniya, to sai a bashi zaɓin wanda zai zauna da shi, watau ko Uwar ko Uban... Idan ya zaɓi zama da Uwar, to sai ya kwana wajen ta amma da rana ya tafi ya zauna wajen Uban sa. Idan kuma ya zaɓi ya zauna wajen Uban sa, to shi ke nan sai ya zauna dare da rana wajen sa.*

*An tsara wannan ne domin yaron zai fi samun tsaro wajen Uban sa inda kuma zai riƙa koyon ilmi (na addini da na sana'a), abubuwan da ba zai samu ba wajen Uwar sa. Idan yaron bai zaɓi ɗayan su ba, to sai a yi masu ƙuri'a".*

**Ana Iya Yarje-Jeniya A Kan Renon Yara?**

Duk da sarƙaƙƙiya da ke tattare da renon yara, ana iya yin yarjejeniya domin tafiyar da al-amarin. Masu haƙƙi a reno, suna iya yin yarjejeniya su saki, ko su daidaita haƙƙokin su. Misali, Uwa da Kaka mace da sauran mata da ke da haƙƙin renon yara, suna iya bar ma Uba haƙƙin kula da yaro ko yarinya ko da basu kai shekarun da aka ambata ba.

**Kula Da Dukiyar Yara**

Shafi na 553 na littafin *al-Hidaya*, Vol. IV, ya bayyana cewa kula da dukiyar yara ya fara karkata ne wajen maza ba mata ba, watau akasin renon su yaran wanda ya fara faɗawa wajen mata ba maza ba. Wannan tsarin an yi shi ne domin maza suka fi dacewa da kula da dukiya musamman ta hanyar sarrafa ta domin ta ƙaru kuma ta bayar da abin kula da yaran har su girma idan masu renon su basu da halin taimakawa da tasu dukiyar wajen kula da yaran.

Littafin *al-Hidaya* ya tsara matakan masu haƙƙin kula da dukiyar yara kamar haka:-

1. Uba
2. Wanda Uba ya wakilta (ko wasiyyin sa)
3. Uban Uba (Kaka namiji wajen Uba)
4. Wanda Kaka ya wakilta(ko wasiyyin sa)
5. Wanda wakilin Uba ko na Kaka ya wakilta
6. Hukuma ko wanda Hukuma ta wakilta. Watau Hukumar Musulunci zata sanya wanda zai kula da dukiyar idan babu Uba ko Kaka ko wakillan su ko wasiyyan su.

A lura cewa, idan yaran marayu ne, kuma babu waɗanda aka lissafa a sama, to, Uwa ko ‘yan-uwan Uba suna iya hawan kujerar kula da dukiyar gwargwadon abinda ake buƙata domin ciyarwa, ilmi, aure da makamantansu. Kuma ko a nan sai idan Hukuma ta bincike su kuma ta amince da su aikata abinda ta hore su a kan dukiyar. Idan kuma Uwar ta yi wani aure to wannan dama ta faɗi ke nan, amma damar na iya komowa idan wannan auren ya mutu. Idan Uwa ko ‘yan-uwan Uba suka ɓata damar su (misali suka yi rashin gaskiya), to sai Hukuma ta koma wajen ‘yan-uwan Uwa domin a samu aminttattun da za’a damƙa masu kula da abinda ya shafi dukiyar gwargwadon abin da ake buƙata domin ciyarwa, ilmi, aure da makamantansu. Kuma Hukuma na iya mallaka ma duk wani daga cikin waɗanda aka lissafa a sama dukiyar baki ɗaya domin kula da ita muddin dai Hukumar ta gamsu da yin hakan ta yin bincike mai zurfi da kuma shinfiɗa hanyar sanya ido a kan yadda ake sarrafa dukiyar.

Abin kula a nan shi ne, wanda duk ya hau kujerar kula da dukiyar yara ko kuma Hukuma ta naɗa shi ya yi haka, to lallai ne ya zamo mai gaskiya da riƙon amana da iya sarrafa dukiya yadda zata bunƙasa, ba yadda zata lalace ko ta ƙare ba.

**RUFEWA**

**نحمده تعالي ونشكره علي نعمه والصلاة والسلام علي رسوله الكريم وعلي آله وصحبه أجمعين**

*Wassalamu Alaikum wa Rahmatul Lahi Ta’ala wa Barkatuhu*